💋 *SALWA* 💋

*STORY & WRITING*
*HAFSAT UMAR DANGORO*

*MARUBUCIYA*👇

*AFNAN*
*AMATULLAH*
*MAR ATUSSSALIHA*
*BABBAR SAKAYYA*
*DEPRESSION*
*BABANA NE SILA*
*UMMU AMANIH*
*ZUCIYATA*
*BURINA MU, AZZALUMI*
*MECE RAYUWAR*
*BA MAHAIFIYATA BACE*
*RAYUWAR KASKANCI*
E..T..C

_*JARUMAI💪🏻WRITER'S ASSOCIATION📚*_
*SADAUKARWA*
*(Sirrina)*

*GODIYA*

*Dukkan godiya su tabbata ga shugaban halitta annabi Muhammad (ﷺ) wan da ya hallaccine ya hallicci dukkan abin dake cikin duniya ,Ina godiya ga Allah suba wanaw wata ala Wanda ya bani baiwa da ikon kawo muku tittattafai dadama ,to ayau ma Nasake samun wata damar da Zan kawo muku kayataccen littafina mai suna 💋 *SALWA* 💋.

*KIRKIRA*

*Littafin 💋 *SALWA*💋 kirkirarene Kuma littafin 💋 *SALWA* 💋 yafarune agaske ba hasashe bane Ina fatan ga duk wadda ta sani damar karanta littafin ta Yi amfani da abin da littafin ya fadakar akai*.

*NOTE*
*Ban amince wani ko wata ya samu damar karanta min book ta hanyar yimin audio batare da

neman amincewa ta ba ,dukkan Wanda ya karanta min shi audio batare da yasanar Dani ba zanyi Shari a dashi domin abimin hakkina*.

💃*MASOYANA NAKUSA DANA KEWAYE KUNA INA!! KUFITO KU GYRA ZAMA DOMIN KWSAR WANAN LITTAFI MECIKE DA DINBIN ABIN AL AJABI, FADAKARWA,TARE DA NISHADANTU WA DA SHI, KAR KU MANTA TAKU HAR KULLUM MAI NISHADANTAR DA KU HAFSAT UMAR DANGORO*💪

*GODIYA TA MUSAMMAN. GA YAN UWA DA ABOKAN ARZIKI HARMA DA MALAMAI NA MASU KARAMIN KWARIN GYWA DA MA MANYANA DA WADAN DA SUKA KASANCE SU GARKUWANE AGARENI MAHAIFIYATA INA MIKA GODIYA AGAREKI UMMANA ,AL,UMMA MA ANA MASU BIBIYATA A TELEGRAM, WHAT'S APP, TIKTOK, AREWABOOKS,FECBOOK, DA MA SAURANSU .
LITTAFIN 💋 *SALWA*💋 ZAI DINGA ZUWA MUKU DAGA KARKASHIN KUNGIYAR 💪JARUMAI 📚WRITAR'S ASSOCIATION✍️
Marubuta masu alki da fasaha da ilimi domin ilimantar da Al,umma*

_*🌘بسم الله الرحمن الرحيم🌒*_.....

_____Dukkan kowacce rayuwa da d'an Adam zaiyi acikin wannan duniyar akwai kaddara, ita Kuma kaddara tana bai bayene da zuciyar d'an Adam, shi Kuma d'an Adam kala biyune, akwai Wanda idan kaddara ta sameshi Yana yadda ubangiji shine Wanda ya Dora masa ita domin yagwada imanin sa,ita Kuma Daya zuciyar Tana kan hanya wadda ta kasance shedan yayi mata da,ira ma,ana zuciyar mutumin da baisan kaddara ba.

Qaddara wata abace wadda ilahirin mutanen duniya ke gudana da rayuwa akan ta, qaddara babban wani abune wan da kan iya sauyawa a kowanne lokaci.

Kuk wani d'an Adam Yana zuwa duniya ne da qaddarar sa,saka makon tun Yana cikin mahaifiyar sa komai da zai wakana a rayuwarsa ubangiji ya gama tsara masa, tam Kar haka ne duniyarmu ke juyawa a kowane irin lokaci.

Musali kamar kaddarar mutuwa kaddara mutuwa itace babban abin da zakayi duba akai idan har ubangiji ya rubuta kaddarar ka yau zaka zo duniya Kobe Kuma ka koma lahira Babu yadda ka iya kokaki ko kaso dole sai ka tafi kamar hakane RAYUWAR Dan Adam ke tafiya dai dai da tafiyar lokaci, Kuma Nima haka tawa kaddarar ta kasance a wannan babban family Wanda ake kiransa da *LAMI'DO FAM* sai dai ta wa kaddarar ta karka tane akan big bro.

## Chapter 1

*TARABA*
*JAIINGO*

*Zaune take a bakin kofar falon idanuwan ta a lumshe bakinta har rawa yake wajan haduwar hakoran ta guda biyu, cikin ka d'uwa da tsoro hawaye masu dumi ke zuba daga cikin idanun ta, hannunta Daya ta dafa tare da shafa kuncinta zuwa wuyan ta tace "inna! "Hannun ta ta sake saukewa zuwa tsakan kanin kafadar ta alamar a furgice take, wata matashiyar budurwa ta hango Tana nufo in da take tun kafin ta karaso gurin ,tayi saurin mikewa tare da fadawa kirjinta ta sake fashewa da kuka, jikinta har rawa yake, a hankula wannan budurwar wadda bazata huce sa,anni da yarinyar ba ta dago da Kai tare da cewa "ya Salam, *SALWA* lafiyar ki Kuwa? Mai yake damun ki Anya ? Naji jikinki kamar a kawai zazzabi, ko ke da goggone? Adda zubai da ce? Ko adda Ameera ce?" girgi za mata Kai kawai salwa take alamar a,ah, cigaba da lissafo mata sunayan 'yan gidan take tare da tam bayar ta Tana cewa "zarah? Ko mufida ce, huzaifa, yaya bilal, yaya Umar? Ko yaya babbace? Khaleesat? Mameyce , ko Amma ce? Kai haba salwa kinsa sai magana nake tun dazu ni kadai Amma kin ki kibani amsa kowa nakira wo kice ba shi bane to wane ko uncle Kabir, abbana, uncle faruq,yaya zaman?" Muryar salwa ta tsinkayo tana yimata magana kamar mai rad'a tace" wannan Aljanin ne Allah ku rabani da shi bazan zauna a gidan Nan ba ni kauyan mu zan tafi" Tana magana tana sake fashewa da wani sabon kukan.

Muryar Amma TA tsinkayo tana cewa "a,ah Ihsan har kin dawo kenan? ,to mai aka Yi mata naganta a haka lafiya?" Ta fada tare da kara sowa kusa da salwa idanun ta nakan Ihsan Tana tambayar ta.

"Wallahi Amma shigowa ta kenan na ganta a bakin kofar falo Tana zaune sai kuka take, Babu irin tambayar da ban mata ba Amma taki fadamin wane wai wani Aljanine, Kuma ni nasan bama da aljanu a gidan Nan"

"Toh" Amma ta fada tare da yin shiru tashiga nazarin aljanu Kuma, can Kuma sai ta tuna da cewa tafa aike TA gurin suhail tun dazu Amma bata ga dawo warta ba sai yanzu da ta ganta anan, kallon su tayi tace "salwa! Ko dai yayanku ne, wan da na aikeki kai masa juice?" Da sauri salwa ta daga Kai tace "Allah Amma aljannan ya fiye kyau da yawa, shi yasan baya son kallo zai na zuwa cikin mutane, mugu kawai Daman ni ya tsana kawai sabi da na kalleshi lemon ya zube garin kallon sa shine ya mareni , har da cemin idan na bari ya sake hada ido da wanan fuskar tawa mai kama da aljanun bururruka sai ya kakkaryani a gidannan" salwa ta sake fashewa da kuka ,sanan ta cigaba da cewa "asani na duk matan kauyan mu nafi su kyau kowa ya ganni saiya kara kallona ,shine shi baiga Yana kama da aljanu ba sai ni, hadda cewa wai nayi irin kwalliyar mahaukata Kuma ni inna ta haka ta kemin"

Amma ce ta sake tallafo salwa Tana goge mata hawayen fuskar ta tare da ruke hannunta sanan tace "kiyi hakuri salwa kinji wata rana sai labari akwai lokacin,akwai ranar kin dillaci dole watarana sai kin rama abin da ake muki a gidannan Kar ki damu kema a hankula wanan kauyancin zai bar jikin ki in sha allah ai babu wan da aka Haifa da iyawa" "uhm uhm Amma ina yaya Abdul tun jiya ban ganshi ba?" "Abdul din Yana gidan Nan kije SA shen goggo mebi Yana cen Dan nasan Babu Inda Abdul yake zuwa daga makaranta sai sashen goggo".

Ihsan ce cikin rashin fahimta ta kalli Amma tace "Amma nifa bangane mai kuke nufi ba akan wa kuke magana wai suhail?yaushe ya dawo?" Ihsan ta fada a tsorace "Bai dade da shigowa ba" Amma TA bata amsa a takaice tare da Jan hannun salwa zuwa part din big bro .

Suna tafe Ihsan Tana bin su a baya har suka karasa wani kayataccen daki mai kyau da keykeli da sallama Amma TA tura kofa sai Kuma tayi rashin sa,a tajishi Yana bathroom Yana wanka ,duk da haka dai bata ji dadi ba ta sake ruko hannun salwa suka fito zuwa part din Amma, kallonta salwa tayi tace" Amma zanje sashen goggo ina son Naga yaya Abdul " tayi maganar cikin shgwaba kamar zatayi kuka.

"Uhm uhm to karki min kuka uwar Sha gwaba ai ba hanaki zanyi ba ,sai kin dawo a gaishe min da goggo".

Bata jira abin da salwa zata ceba kawai tasaki hannunta ta cigaba da tafiya ,salwa ce TA juyo ta kalli Ihsan tace "zanje gurin yayana idan mun gaisa zan dawo " shiru tayi Ihsan batare da tace mata komai ba ,da kamar ta hanata zuwa sai Kuma ta kyleta tun da bata gaji da kukan ba, Dan tasan su adda zubaida suna can Kuma tasan baza su wanye kalauba.

Tom Kai rsaye part din goggonsu ta nufa tun daga bakin kofar falon taji gaban ta ya fadi jikake dummm ,da kamar ta koma ganin yadda kowacce a cikin su ta zubo mata ido suna watso mata harra musamman ma adda Ameera wadda ta sake hade girar sama da ta kasa lokaci guda, hanjin cikin salwa ne ya sake kadawa cike da fargaba ta soma taka falon kamar wata munafuka Tana bin bango, sai da tayi rabin fita daga falon adda zubaida ta kwalla mata kira tare da cewa "ke jakar kauye zonan" hucewa tayi tare da yimata banza bata kula suba,sai jin muryar adda Ameera tayi tace "Ke salwa ba dake muke ba baki jin magana ,bamu isa muce kizo bane? Shegiyar yarinya mai kama da aljanu jibi wani shiga kamar mahaukaciya riga daban zani daban ,jiwata shegiyar kwalliya kamar ta mahaukata" takara sa maganar daidai lokacin da salwa ta karaso gurin ta durkusa gywarta a kasa tace "adda zubaida gani" hannun ta zubaida ta kamo tare da hade rai ta sharra mata Mari tace "Dan uwarki bakiji ina kiranki ba kika shareni ni sa,ar kice?" "Dan Allah kiyi hakuri wallahi ban San Dani kike ba, naji kince jakar kauye nazata ko a t.v kikaga jaki kike fadin haka" tayi maganar ta na zub da hawaye tsabar Jin zafin marin da

ta mata.

"Eyyee ah lallai yarinyar to Dan uwarki daga yau kece jakar kauyen ba jaki ba, kinji ni shasha Sha, da wakike tunanin zan kalla anan nace jakar kauye idan ba ke ba ko munmiki kala da rainon kauye? Baza ki daina tsareni da wadannan idanun naki ba sai kin cinyeni mayya kawai?" Shiru salwa tayi mata batace komai ba tayi kasa da idanun ta Tana goge hawaye, khaleesat ce tace "haba adda zubaida Dan Allah kiyi hakuri ki cika ta kinga dai Babu abin da tayi.... Ai bata karasa maganar ba zubaida ta daka mata tsawa tare da cewa "shiiiii idan ina magana kina saka min baki saina ci ubanki wallahi Sha Sha Sha kawai" dawa tayi da kallon ta ga salwa tace " jakar kauye ina Zaki?" "Uhm uhm da damn... "Dakata ni zakiyiwa Sha gwaba tambaye ki fa nayi ina zaki?" "Gurin yaya Abdul zanje" tafada a takaice.

Uhm adda Ameera tayi wani irin murmushi sanan tayi kwafa tace "ke wai uban mene hadinki da Abdul ? Kewai wace iriyar ballagazar matar aurece kije wajen mijin ki mana uban wa ya hadaki da Abdul ?" "Uhm Nima wallahi Ameera abin Nan Yana bani mamaki mijin ta da ban wan da ta makale wa daban, ko da yake shi big bro da wann auren da Babu duk Daya idan ban da su Abba ma uban mai yaya zaiyi da da wanna jakar kauyen dukkan mu gamu a zube a aura masa mana sai wanna karamar yarinyar da batasan komai ba ai wallahi yanzu na soma gana miki azaba tun da har ki ka shiga Gonata, kitaho tun daga kauye kizo ki auremin abin da na fiso a rayuwa ta ai wallahi baza ta sabu ba"

Mufida wadda tun da suke abin su bata saka baki ba sai da aka zo maganar sahibin ta tukunna tace "ni wallahi har yanzu inajin ciwan wanna abin da akayi Mana' haba arasa wadda za a aurawa yaya suhail sai wanna jakar kauyen ai wallahi Indai ina raye saina kashe aurenan " "nooooo ai ba sai kin kashe shi ba zai mutu murus tun da dai banga mai zaiyi da wanna abin ba ,bakiga ko kallo bata ishe shi ba "cewar zarah wadda ta karasa maganar tare da dumawa salwa duka a baya.

Ameera ce ta sake kallon salwa tace " tashi mu ki bamu guri tun kafin mu kashe ki a gurinnan shasha Sha mai bin maza duk tabi ta mallake zuciyar mazan gidannan".

Ita dai salwa batace komai ba ta kama hanya jiki a sanyaye ta shige kofar da zata sada ta da dakin goggonsu.

Tana shiga dakin ta tarar da goggo a zaune shi Kuma Abdul na kwance ya Dora kansa a kan cinyar goggo Yana Dan Danna waya, kamar an jefota ta fado tare da cewa "Assalamualaikum?" Durum gaban Abdul ya fadi a take yayi wata iriyar zabura Jin muryar Abar kaunar sa, ita kanta goggo sai da ya tsorata ta da zaburar da yayi, a razana tace "ABDULHAMEED lafiya?" Shiru Abdul yayi mata baice komai ba, saima mikewa da yayi zaune yace "wa alaikumussalam da auntyna" harara ta watsa masa tare da turo baki gaba ta karaso gaban su, ta fada kan

goggonsu sanan ta saki kuka tace "goggo kinga yaya ko kice ya daina tsokana ta bana so" dariya goggo ta bude baki zatai sai Kuma TA dakata ganin yadda shatin Mari ya fito rad'o_rad'o a fuskar salwa , hadiye dariyar goggo tayi tace "ummeetarh yanaga fiskarki a haka waye ya mareki?" "What' mari Kuma "Abdul ya fada a razana tare da kafe fuskar salwa da ido Yana jiran yaji wan da ya taba ta.

"Uhm uhm goggo Babu kowa bugawa nayi" wani mugun kallo Abdul ya watsa mata ,har sai da Tasha jinin jikin ta tace"am am yaya fa gaskiya....... "Shiiiii da kata Salwa waye ya mareki na tambayeki ba karya nace kiyi min ba abin da baki saba Yi ba shi kikeso ki koya, salwa bansan ki dayin karya ba mai yasa kike son ki cuci kanki ne idan bakya son kanki ai mu muna sonki eh, ki fadamin waye ya mareki ko yaya ne?"

Shiru salwa tayi daga bisani Kuma ta Dan ja dogon numfashi tace "kayi hakuri yaya Abdul Dan Allah idan na fadama ka kada ka musu wani abun" tayi maganar Tana d'an rausayar da Kai alamar shagwaba , "uhm Tom shikkenan naji bazan daki kowa ba" "uhm uhm yaya Daman adda zubaida ce ta mareni ban mata komai ba" "baki mata komai ba sabi da cin zali shine zata mareki ? To taso muje inga uban da ya tsaya mata har ta mareki" ya mike tare da ruko hannun salwa Yana janta har suka fita falo, yanajin goggo tana cewa ya bari ya dawo Amma yayi mata shiru ya ciga ba da tafiya.

Yana zuwa dai dai in da suke a zaune ya tsaya fuskar Nan a daure kamar Daren mutuwa, itako adda Ameera hadda wani gyra Dan kwali sabi da tagan shi,shikuwa ko kallo bata ishe shi ba, "ke uban mai tayi miki kika mareta?" "Am am yaya Daman "shiiiii Daman mai metayi miki kika mareta nace?" "Yanzu yaya ni ban Isa na hukunta salwa ba idan tayi laifi?" "Laifi 'yarki ce dazaki mareta, ko sa,ar kice ayanzu tafiku matsayi da daraja tun da ita Tana da igiyoyi uku a kanta sabi da tsabar rashin mutunci shine Zaki mareta" "oh Al duk acikin auren ne ka kama hannunta karike sai kace wata matar ka" zubaida ta fada a zuciya afili Kuma tayi shiru. Sa kamakon Jin takun da idan taji shi Yana daga mata hankali da Kuma tafiya da dukkanin hankalin matan gidan shine takun abin da sukafi so a rayuwarsu ,big bro kenan.

Daga shi sai jallabiya fara fuskarsa dauke da saje wan da yayi mugun kara masa kyau hade da wani lallausan gemu girar fuskarsa wadda ta kasance a hade da Daya ya daga lokacin da yayi ido hudu da hannun salwa da Abdul a hade, Kare tamke Rai yayi ya cigaba da tafiya abin da har ya karaso in da suke, kallon Abdul yayi Shima Abdul din kallon sa yayi yay saurin cewa "barka da fitowa yaya" banza yayi masa tare da wurga masa harara lokaci guda Abdul yayi saurin hadiye wani yawu jikuke kukukuuut gaba ki Daya yasha jinin jikinsa, da sauri ya saki hannun salwa ya kara matsawa gefe, shikuwa Suhail kallon salwa yayi kamar wan da yaga mutuwa yasake hade rai yace "keeeh...."ai kafin ya karasa fadar abin da zance salwa ta watsa a guje har Tana gware Kai wajen fita daga falon, girgiza Kai kawai suhail yayi ya huce domin shi abin ma dariya ya bashi, Yana jin su zarah na gyshesa yayi musu banza baice komai ba ya

huce gurin goggo, shi Kuwa Abdul salwa yabi abaya da sauri har ya fita daga falon bai ganta ba hakan yasa ya huce sashen su Ihsan  Dan yasa can ta nufa.

💋 *SALWA* 💋

*©HAFSAT UMAR DANGORO*

Chapter 2

Su Kuwa su zubaida,Abdul Yana barin gurin suka kwashe da dariya tare da cewa "Amma dai anyi asarah wallahi ,jibeshi Dan Allah yadda yawani bita kamar wani jela"  ita Kuwa mufita kallon Ameera tayi tace "oh Amma dai Ameera kinyi asara yanzu sabi da Abdul din kika zauna kina kuka kin badani" wallahi idan nice sai na bari bayanan zan lakadawa shegiya duka" cewar zarah "uhm bazaku Gane ba, gwara nima iya kacin kuka nayi kukuwa fa tsabar asara kuna faman masifa akan mutum daya kune manyan asarar ru" matseatsatssss Ameera tayi tsaki ta bar gurin.

A bangaren Abdul Kuwa Yana karasawa part din Amma Kai tsaye dakin Ihsan ya shiga, ko sallama babu tsabar tashin hankali da Jin tsoron abin da ya faru da salwa lokacin da ta buge, zaune ya same su Ihsan na cewa "haba salwa mai yake damunki kema sai kace bakisan ciwan kan ki ba na fada miki ki hakura dazuwa part din goggo kin ki kiji, yanzu GA irin tanan jibi kanki yadda ya kunbura tsabar mugunta Harda gwara miki Kai sukayi" a hankula salwa ta soma magana cikin sanyin murya Tana cewa "Ihsan narasa mai nayi ma su adda suka tsaneni bansan mai yasa ba ko kaddara tace a haka ,nifa bani na nace su Yaya Abdul su soni ba , ubangijin da ya haliccemu ni da Abdul shi yasan yadda zaiyi damu, naso ace Abba da yatashi Abdul ya auramin a matsayin mijina ko Babu komai zan rage wani kunci da zafi na maraici ,sai dai kash Allah ya hadani da Wanda take ganin shi yafi dacewa Dani ,nasan cewa yaya suhail jininane Amma shi bai San haka ba baya duba dangantaka ta dashi, a kullum zuciyarsa na raya masa cewa yafi karfina mai zaiyi Dani sabi da ya na ganin ni ban Kai ya zauna Dani a matsayin mata ba, wallahi Ihsan ko da ace sakina yaya suhail yayi bazan Yi kuka Dan ya sakeni ba ,zanyi kuka ne akan cewa ya mai Dani karamar bazawara" daga haka salwa ta fashe da kuka, gaba ki Daya jikin Abdul ne yayi sanyi lokacin da yaji magan ganun salwa, bai taba tunanin salwa Tana da hankali da manyan taka irin haka ba, salwa yarinya ce karama sosai wadda za a iya cewa batasan mai take a yanzu ba, shi Kansa yanajin cewa inama a dawo da auren ta Kansa ,da ya nuna mata gata Wanda har a bada bazan ta tabajin ita marainiya bace sai dai In ko tunawa tayi, sai dai Allah yariga  ya tsara salwa matar big bro ce, Babu yadda ya iya bazai ce zaiyi kishi da yayansa ba ko Babu komai yasan watarar yaya suhail zai sota.

Batare da Abdul ya furta komai ba ya mike jiki a sanyaye ya bar dakin itakuwa Ihsan bin

bayan sa tayi da kallon tausayawa Dan tasan irin kaunar dake tsakanin salwa da Abdul kwata kwata da dawowar salwa gidan baifi wata 6 ba Amma jibi yadda sukayi sabo har basa so su rabu.

Kallon salwa tayi tace " salwa sunanki Yana nufin farinciki da kwanciyar hankali, yakamata ace kazama mai farinciki a Koda yaushe kizama mai kntar da hankali akan kaddara kiyi hakuri,kinji ki daure kiyiwa uncle biyayya amatsayinsa na mahaifinki kinga dai uncle baya raye, Allah ya karbi rayuwarsa ya kamata ace kin Yi kokarin cika masa burinsa ki zauna da yaya suhail ko Babu dadi ki nasa biyayya iya kacin iyawar ki kada ki Gaza akan haka Kuma Kar ki kuskura Koda da barin bakine kice big bro ya sakeki, kibari ya sakeki da kansa duk da bana fatan haka, domin wallahi kinyi dace acikin mata dubu ke Zara ce yaya suhail mata basa gabansa ,kina dai ganin yadda matan gidan Nan ke bin sa suna sanshi Amma shi ko a jikinsa bama tasu yake ba, Kuma nasan Babu abin da suke yiwa sai kyaun da Allah yayi masa da Kuma kudi, duk da kasance war yaya suhail yayanane jinake kamar in boyeshi na dinga ganinsa kullum, sainaji inama nice nasamu wannan damar da kika samu ,sai dai kash Allah kenan saiya hadani da shi Amma Kuma a matsayin yaya da kanwa, kije kiyi sallah Naga lokacin sallar azahar yayi idan kin idar sai kizo muje part din big bro muyi masa sannu da dawowa" zaro ido waje' salwa tayi tace " wa ni  in Zaki ki bar jirana .in kinganni a lahira kaini akai wallahi bazani ba sai kin dawo". Daga haka salwa ta mike tashiga bathroom.

Bayan ta Yi wanka ta dauro alwala, sosai da tafito Naga kyen yarinyar ya karu sabi da ta wanke kwalliyar 'yan kauyen, bakin drowa ta matsa tare da bude murfin drowar ta dakko wata doguwar riga pink mai rashin fari, mai kawai ta shafa Sannan ta saka rigar hadi da fesa turare a jikin rigar da Kuma hijabin ,daga bisani Kuma ta shin fida daddumar ta tayar da sallah.

Ita Kuwa Ihsan part din big bro ta shiga ,kwance ta sameshi a kan bed ya cire jallabiyar ya ajiye a gefe, idanun sa a lumshe da alamun dai babacci yake ba sabi da idonsa na San motsawa Kuma yadda ya ke a kwance kamar tunanin wani abun yake, cikin nutsuwa Ihsan ta karasa hadi da cewa" yaya barka da wannan lokacin" shiru yayi bai ce mata komai ba Kuma har lokacin bai bude idonsa ba, sai da ihsan tacire Rai da zai amsa mata sai Kuma taji yace "yakike? A nutse ya sauke idonsa a kan ta yace "ihsan " "Naam yaya Naga kamar baka jin dadi, nazo gurinka nayi maka oyoyo Amma sai nagan ka wani iri, yaya da kwarin gywata na taho Amma kasani naji jikina yayi sanyi mai ke damunka?" "Uhm kanwata kenan Babu komai" daga haka ya juya ya yadauki wayarsa ya shiga dannawa ,itakuwa Ihsan idanun ta na kan abin da yakeyi, a yadda ta kula ba abin da yakeyi kawai dai Dan Kar ta sake tambayar sane ya dauki wayar, jiki a sanyaye ta mike tare da cewa "yaya sai anjima" batare da yace mata komai ba tafita.

Tana fita ta ci Karo da Amma zata huce, da sauri ta soma kakaro murmushi a fuskarta tace "Amma ! "Naam Ihsan lafiya kuwa naganki a haka kodai ke da Suhail ne" sun kuyar da Kai Ihsan tayi zuciyarta na raya mata shin ta fadawa Amma abin da ke faruwa kokuma ta zubawa abin ido taga iya Inda wasan zai tsaya, bata gama tunanin ba Amma ta sake cewa"Ihsan bakice ko mai ba?"

"Uhm Daman Daman Amma yaya suhail ne Naga Yana cikin damuwa Kuma..." Kuma mai, kijini da shashashar yarinyar kin kasa fadamin magana " "uhm Amma na fahimci yaya bayason auren Nan ayanayin da na fahimce shi ba zai iya sanar da ku bane Amma baya son auren salwa ina ganin Amma da hakura akai, kuma itama salwa bata son yaya hasalima tsoransa take, ni a ganina kawai tun da Naga ya Abdul na son ta kawai a mai da auren kan ya Abdul"

"Mai Abdul baki da hankali Ihsan har yanzu ka yarinya ce, shi suhail din ne yace miki baya son salwa to idan bai so taba wazai so, ko ita salwan ce tace miki bata son shi?"

"A,ah Amma kawai fahimtar haka nayi" "uhm kawai Amma tace Sannan tace "kihuce daki, Kuma ki daina damuwa akan haka kinji dukkansu suna son junansu fatanmu dai Allah ya hade kawunan mu baki daya" daga haka Amma ta huce ita Kuma Ihsan ta huce part din su.

A bangaren salwa Kuwa bayan ta idar da sallar ne ta daga hannun ta sama idanuwan ta na zub da hawaye, murya na rawa ta ke cewa "Allah kagani bani da tsumi Kuma bani da dabara, ni baiwar kace mai tsananin bukatar kulawa da nuna soyayya a gareni, tun ina cikin mahaifiyata nasa ba da kaunar da take nunamin, har Allah yasa Nazo duniya, yanzu gashi ta tafi ta barni ,Allah kaga halin maraici da nake ciki ba uwa ba uba ba kaka, Allah Kashi ga lamarina, ban San dalilin da yasa na kasance a matsayin matar yaya suhail ba bayan nasan baya Sona Kuma bazai taba son mace Irina ba, domin nasan yafi karfina, Amma a haka ubangiji kayi ikon ka a kanmu ka mallaka min shi ,sai dai har yanzu ban samu zuciyar sa ba, sai Kuma ka dorawa ka ninsa soyayyata bayan kasan ni matace a gurin yaya suhail, na kasa Gane me hakan yake nufi ya Allah kayi gaggawar warware min wannan lamarin, akullum kara Sona da kaunata mazan gidannan suke duk da bansan irin baiwar da kamin ba, Amma nasan ni macece mai hakuri ,Kuma zanci gaba da hakuri har izuwa lokacin da kaddarata zata sauya" Sha fawa tayi Sannan ta cigaba da yin kukan ta.

Ihsan Kuwa dake tsaye a bayanta batasan lokacin da hawaye kebin kuncinta ba ,sabi da tsananin tausayin salwa, jiki Babu kwari Ihsan ta karaso kusa da salwa tare da kama hannunta.

A furgice salwa TA dago San bata San da mutum a bayan ta ba, Tana dagowa suka hada ido da Ihsan saurin goge hawayen fuskar ta tayi tace "Ihsan lafiya yaushe kika dawo, ina big bro din?" Salwa ta watsomata tambayoyi lokaci guda.

"Uhm salwa !"
"Naam Ihsan "

"Kinason yaya suhail?"

Drumm gaban salwa ya fadi zuciyarta ta shiga har bawa, cikin rashin sanin mai zata ce mata tace "ba b ban bangane mai kike nufiba?"

"Uhm salwa kinason yayana ko?"

Kukan salwa ne yasake tsanan ta cikin shashshekar kuka tace "wallahi Ihsan ina son yaya suhail Amma banason kowa yasan wannan maganar dagani sai ke, tun kafin na soma saka Yaya a idona na so shi, na soshine tun kan nasan waye shi ya kamannin sa suke, akullum mahaifina bashi da aiki sai bani labari akan yaya suhail Yana cemin, 'yata kin San mai, yayanki fa Yana gaysheki Yana Nan yace zai zo ya ganki ,zai kawo miki 'yar tsanar wasa, zai siya miki alewa yace . "Kullum Abba cikin yimin maganar yaya yake, wannan kaunar da yake nunamin yasa na soma kaunarsa tun kafin nasan mai Nene so ,tun kan na ganshi nake son shi Ihsan, wallahi Ihsan Kar kice soyayyar da nake masa ce yasa abbana ya bada wasiyar a aurawa yaya Ni, ko kadan, abbana bai San ina son yaya suhail ba abu Daya yasani shine Yana son yaga ya hada zumunci" tsayawa salwa tayi da maganar ta share majina Sannan ta ci gaba da cewa " ihsan na shiga uku soyayyar yaya suhail itace ajalina nasani, ban taba tunanin soyayyar da yaya yakemin zata koma kiyayya ba sai bayan an daura auren mu, ban sani ba ko Dan ganin idon abbana Daman yake Sona oho, idan nace miki jiya na fara saka yaya suhail a idona Zaki yarda, a jiyane nasan kamannin yaya Kuma ajiyan naji soyayyarsa ta kara nun Kuwa a cikin zuciyata, ki fadamin mai zanyi akai wazan kaiwa kukana ,bazan takura dole yaya sai ya soni ba Amma ni nasan ina da wan da ya halicci yaya tun da ina da ubangiji shi kadai yasan dalilin da yasa rayuwa ta ta kasance a haka"

Shiru Ihsan tayi tsabar mamaki da Kuma tsananin tausayin salwa,tabbas akwai babban aiki a gaban salwa sanan a kawai yaki, domin iya su adda zubaida kadai aka bar salwa da su sai sun Kai TA kasa to Amma shi yaya suhail wai wayake sone, meyasa haka eh , ko Dan Yana da kyau ne, Ihsan ta fadi haka a zuciyar ta a fili Kuma tace " kiyi hakuri salwa kici gaba da addu,a akai Nima zan tayaki addu a kinji " "in sha Ihsan nagode Amma Dan Allah wannan maganar ta zama sirri a tsakani na dake" "in Sha Allah bazan fadawa kowa ba".

"Yanzu dai ki je inji Amma " to kawai salwa tace ta mike ta fita, bayanta Ihsan ta bi cike da tausayawa ,Sannan ita ma ta mike ta dakko wayarta, ta soma dannawa.

.......................

Mamey ce zaune a part dinta ta harde kafa Daya kan Daya hancin Nan nata ya sake tashi sama sabi da tsabar masifa, ita Daman aba ba kyau ba sai ta sake yin muni ,cikin masifa ta ke kallon Ameera tace "uban mai kikeso yanzu nayi miki , kinzo kin Sakani a gaba sai kace zan

wadda zan bawa mama, shashasha kawai ace wai 'yar qauye tazo tafiki iya Jan hankalin namiji ,ai wallahi ban taba sanin Ameera ke shashasha bace sai yau ,yanzu salwa Zaki tsaya kinawa kuka, salwa? Nawa take yarinyar to ina ruwanki da son da Abdul yake mata, ai abanza salwa dai matar aurece koyaki ko yaso haka zai gaji ya hakura ,tun da Tana ganin suhail bazata zabi Abdul ba ,Kuma wallahi Shima Abdul din sainaci ubanshi kamar yadda ya kuntata min saina kuntatawa uwarsa ,itama Ihsan din sai dai ta mutu Indai sai ta auri huzaifa ne, bari huzaifan ya dawo Naga ta tsiya"

Kuka Ameera take Tana cewa" ni wallahi mamey ba salwace tafi batamin Rai ba ,irin yadda su adda zubaida suka zauna suna cikin mutunci akan Abdul,wai nakasa samun zuciyarsa su basuga yadda yarinya karama ta hanasu kwanciyar hankali ba, jibesu fa mamey kusan su hudu duk akan big bro kowacce son shi take ,ai yasin gwara ni so dubu" .

Uhm "dallacan ni rufemin baki duk ai jirgi dayane ya kwasoku Kun bi kun makalewa 'yayan mutum daya kamar su kadaine mazaje a duniya, baga sauran 'yan uwanku Nan ba duk gasu Umar ,bilal, zaman ,sauban Khalid ,huzaifa , Amma duk Kun nacewa Abdul da suhail , idan ban da asra ma ke zarah,wai Abdul kukeso kuna uwa Daya uba daya sabi da namiji kuna gaba ,wallahi Kun bada mata, su Kuma wadan can asararrun zubaida, mufida,zarah da Kuma wancan aljanar matar salwa tashi wai duk kansu akan suhail,Allah ya raba bawa da wahala, tashi ni ki bani guri mara zuciya wadda batayo halin harziki ba".

Ita dai Ameera bata sake cewa komai ba ta mike ta nufi Dakin su.

Tom salwa Tana Isa part din Amma, ta Yi sallama, Amma ce ta amsa mata sallamar Sannan tace "A,ah salwa karaso mana" salwa ce ta karasa fuskarta dauke da murmushi ta cewa " Amma ina wuni?" "Lafiya kalau salwa, Daman cewa nayi kizo ki kaiwa suhail abinci tun da Naga yanzu kina matsayin matarsa bai kamata ace ni ko Ihsan muna Kai masa ba" durummm salwa taji gabanta ya fadi lokaci guda tanemi duk wani kuzarinta ta rasa jikinta yayi sanyi ,saka makon tunowa da maganar da ya fada mata cewar kada ta sake bari yasake hada ido da ita, Amma ce ta fuskanci kamar akwai wani abu ganin haka yasa tace "salwa lafiyarki Kuwa yanaga lokaci guda duk kin sauya?" "A,ah Amma Babu komai Yana ina abincin " batare da Amma TA ce komai ba ta mike ta dakko mata abincin a plate ta bata Sannan ta koma ta zauna, ita Kuwa salwa mikewa tayi ta nufi hanyar fita jiki a sanyaye ,kofar ta janyo tarufe Sannan ta nufi hanyar da Zara sa data da part din big bro.

Amma Kuwa, zama tayi tai shiru daga bisani Kuma tace "tabbas akwai abin da yake faruwa a tsakanin yarannan, Amma.. Babu komai nasan yadda zanyi.

Salwa ce tsaye a kofar dakin big bro ta tsaya tayi tsuruu takasa motsawa ita bata shiga ba ita

bata matsa daga jikin kofar ba, gashi ta jingina a jiki ta kalli sama ko mai take tunani oho, suhail ne tsaye a tsakar falon yasha farar riga da wando baki dogo, sai gashin sa da ya taje yasa hannu ya nad'esa a bayansa, wani bakin glas ya Dora a idonsa wan da ya kara masa kyau da kwarjini, yayi kyau sosai ko ina zaije? hannunsa rike da kee, hannu yakai kan kofar tare da budewa, ai kafin ya an kara salwa TA fadi kasa, shikuwa abincin gaba ki d'aya yayo kan sa ,abin ka da Miya duk ta bata masa farar rigar, hatta juice din sai da ya sheko masa jiki, ran sa in yayi dubu ya baci, ita Kuwa salwa a tsorace take binsa da ido jikinta narawa sabi da tsoro, gaba ki Daya tabi ta manne a jikin bangon dakin Tana kallonsa kamar wani mayunwacin Zaki,sai huci yake, gumine ya soma zubo mata, allah sarki duk da AC dake dakin hakan bai hanata gumiba tsabar kaduwa da tashin hankali.

💋 *SALWA* 💋

*©HAFSAT UMAR DANGORO*

Chapter 3

Big bro Kuwa abin duniya ya isheshi yama rasa mai zai mata ya huce, hannunsa yasaka ya janyota gaban sa tare da zama gefen kujera, ya kuramata ido Yana kallonta cike da tsantsar tsana, idanun ta ta sauke a kasa hadi da hade hannayen ta guda biyu hawaye nabin kuncinta ,sai yanzu ta tattaro duk wani kwarin gywarta tace "Dan girman Allah yaya kayi hakuri, wallahi bansan zaka fito ba, Dan Allah Yaya kada ka mareni, wallahi bani bace nazo Allah yaya Amma ce tace na kawo Maka abin ci ,Kuma Nima sai da nayi tunanin bazan zoba sai tace Al Kai miji..... "Shuruuuuuuuu......... Nace, shasha Sha uban waye mijin naki ni.... Ya sake hade rai yace "wallahi idan bakiyi wasa ba saina kakkaryaki a gidannan ni sa,Anki ne? Waya baki IZININ zuwa part Dina, ban ce miki ko ido karki sake bari muhada ba, wato ke uwar taurin Kai hadda shigomin daki Are you monkey?" Kukan da salwa take ne yasake fitowa fili sabi da tsabar Jin zafin magan ganun da yake fada mata, wai yau itace ake ciwa mutunci haka, Kuma wai yayanta wan da yake mutuwar nuna mata soyayya ada shine ayanzu ya dauki tsanar duniya ya Dora mata, Wayyo ni salwa maraici bai ba nasan da ace abbana yana Nan Babu mai kawoni Nan har aci mutuncina, tsawa yasake daka mata ganin yadda tayi masa shiru batace komai ba ,wato ta ma maida shi mahaukaci, "keeeh..... " Da sauri salwa TA dago suka hada ido, wani irin yarrrrrrrr.. taji jikinta ya soma bari kamar ganga, gaba ki Daya TA 'kame guri Daya lokacin da tayi to zali da kwayar idonsa, sumar zaune tayi ta tsaya cak a haka, ai Kuwa batai aune ba taji wani saukar gigitaccen Mari a kuncinta ji kake tasssss tasssss, Allah sarki baiwar Allah gigice war da tayi ne yasa takasa Gane inane gabas inane yamma, gaba daya idanunta duhu take gani sabi da tsantsar azaba batasan lokacin da ta cakumo rigarsa ba ta rungume shi, tare da kan kameshi sosai a jikinta, numfashin ta nawani irin fita, zuciyarta kuwa sai bugu take kamar ganga.

Saurin janyo ta yayi daga jikinsa hadi da cewa" ya Salam... Shi Kansa ta tsoratashi ganin yadda ta gigice kamar wadda taga wani bakin aljani, shiru ya danyi Yana kallon yadda take

motsi cikin furgici a kirjinsa, sai lokacin ya tuna cewa fa shi sojane Kuma shi Kansa yasan ko namiji ya mara ba karamin Jin jiki zai ba, balle Kuma salwa da tun da yake asanin sa 'yar gatace gaba da baya Babu wan da yataba marinta, cike da tausayin ta ya sa hannu tare da tallafo bayanta Yana shafa fuskarta dai dai gurin da ya mareta, A hankula yake Kai bakinsa saman kuncinta Yana Dan hurawa gurin iska ko zataji sassaucin marin, itakuwa salwa ajiyar zuciya ta shiga saukewa hawaye masu zafi nabin kuncinta, shi Kansa suhail din jiyayi kamar yasaka kuka, ganin irin zalicin da yayiwa kanwar tasa, lokaci guda ya shiga tunano irin soyayyar da abban salwa ya nuna masa, gaba kidaya sai yaji jikinsa duk ya mutu.

Lokaci guda ya tsinci kansa da son bata hakuri Amma girman Kai da takama ya hana shi, sai aikin bin ta da kallo.

Cikin mintina kalilan bacci ya dauke salwa sabi da tsabar wahala, har baccin dole tayi, shikuwa big bro a hankula ya saka hannun sa gaba daya ya dagata cak kamar wata 'yar baby yayi bedroom da ita, bai ajiye ta a ko inaba sai kan katafaren gadonsa na alfarma, sai dai so yake ya janyeta daga jikinsa Amma yakasa sabi da ta kanka mesa gaba daya, shikuma bayason ya tasheta balle tasake masa wani kukan, Dan haka ya hakura ya kwanta Shima a kan bed din tare da yin rubda ciki,  salwa Kuwa har yanzu hannunta na makale a jikinsa.

60:30 pm ___________________

Shiru_Shiru salwa bata dawo ba ,Dan haka Ihsan ta mike ta nufi gurin Amma a zaune ta sameta, ta idar da sallar magriba, Tana addu,a ,sai da ta bari ta idar tukunna tace "Amma ina salwa taje tun dazu da kikace na kirata har yanzu bata dawo ba" mamaki ne ya kama Amma Jin wannan magana daga bakin Ihsan,cikin rashin fahimtar mai take nufi Amma tace "ban Gane ba ? Zan kwdanta ta na cinye ne, ina tun dazu ta dawo " "tadawo Kuma Amma daga ina kenan?" "A,ah dazu na aiketa wajen suhail tun rana takai masa abinci ,Kuma Tana zuwa ko minti 5 batai ba na bata abincin ta Kai masa, Kuma kice haryanzu bata koma ba to ina taje kanan?" "A,ah wallahi Amma bata dawo ba ,Amma bari na je gurin ya Abdul ko Tana can" shiru Amma tayi tana tunani can Kuma bayan futar Ihsan itama ta mike, part din big bro ta nufa kartaje 'yar mutane ta bata, Tana zuwa taga kofar a bude, da kwanukan abincin ta soma tozali Inda ya bare a haka suka tafi suka barshi, falon ta cigaba da bi da kallo, har zata juya saikuma, ta mike tanufi bedroom.

Durum tayi ta tsaya tana kollon ikon Allah hadi da mamaki da Kuma damuwa kwance akan fuskar ta, a hankula ta furta "lallaima yaronan" kwafa tayi kawai ta fita.

Tana fita suka cikaro da ihsan abakin kofa zata shigo, kallonta Ihsan tayi tace "Amma ina Ihsan din kinganta? Naje ban sameta a gurin ya Abdul ba"  "Kar ki damu ina son yanzu kije ki fadawa kowa na gidannan akwai taro anjima a part din goggo" "toh... Amma mai ya faru haka,

ina salwa?" "Ba tambayata nace kiyi ba ina son yanzu kije kiyi abin da na saka ki" Babu musu Ihsan ta fita zuciyarta cike fal da tunani.

Itama Amma sama ta haye tare da mikewa wata kofa wadda ni kaina ban San waye a cikin ba Kuma bansan mai zatayi ba, tana zuwa ta tura kofar tare da yin sallama, daga ciki aka amsa da "wa alaikumussalam" cikin muryar dattako, karasawa tayi Inda yake ,Yana zaune a bakin gado kekkewan dattijon mai kyau ga ilimi da kuma haiba, zama tayi tare da sakar masa murmushi tace " barka da dare *ABU SUHAIL* " murmushi ya mai da mata tare da cewa "Barka dai *AMMAN SUHAIL* ya naganki kamar kina cikin farinciki kodai wani abune yafaru ?" "Uhm abu suhail ba dole nayi farinciki ba ranka ya dade ai kaima wanna albishir ne mai gwabi yalla bai" dariya Abba yayi yace "toh ina jinki ranki yadade Maza fadamin" "magana ce akan auren salwa da suhail da muke ganin kamar bazasu kaunaci junan su su zauna a tare ba, ada munso mu raba auren tun da munga tsakanin Abdul da salwa sunfi shakuwa, sai a maida auren kan Abdul , to Kuma yanzu na aiketa ta kaimasa abinci sai naji shiru,nabi bayanta,anan ne na samesu a kwance manne da juna cikin so da kwauna suna bacci" zaro ido Abba yayi yace "wai Dan Allah dagaske kike ?" "Dagaske nake ranka shi dade" murmushi Abba yayi ya mike tare da durkusawa kasa yayi sijjada, a hankula ya furta "Alhamdulillah, yanzu Maza a hadamin zama a gidannan domin musanar da ranar tarewar su" "ai na aiki Ihsan lokacin da na hawo sama zuwa bayan Isha,I kowa zai hadu a sashen goggo".

Tom acan bangaren suhail da salwa Kuwa, bacci yayi nisa sun dage sai Jan munshari suke , abin ka da ba a sababa sun wani makale junansu kamar wasu masoyan Gaske.

Misalin karfe' 8:00 na dare ,ilahirin familyn LAMI'DO na zaune a sashen goggo, kowanne acikin su yayi shiru Yana tunanin Maine dalilin da yasa aka hada taron, musamman mazan gidan su Umar da bilal zaman sauban Khalid huzaifa duk sunyi tsit kowanne kirjinsa na bugu,Abdul ne ya shigo tare da goggo suma gefe suka samu suka zauna suna jiran shigowar su Abba.

A can bangaren su suhail kuwa,salwa ce ta mike a furgice ganin yadda ta ganta a kan gadon big bro Babban abin mamaki da fargabar ma yadda ta ganta a jikinsa a rungume, baki ta kwabe tare da fashewa da kuka, da hanzari Shima suhail ya mike tare da kafe ta da ido cikin masifa yace "keeh lafiya?" "Uhm uhm yaya Maine hakan zaka tabani, wayasa ka kawoni dakin ka, Daman Kai Dan iskane?" Ta fada a shagwaba,shi Kuwa suhail tsabar takaici ma yarasa mai zaiyiwa yarinyar ya huta da bakuncikin ta, wata uwar harara ya watsa mata yace " to uban mai zanyi dake, mai zan taba a jikin naki, ki bari kizama mace tukunna sai kiyi ikirarin na tabaki .... Bai gama maganar ba yaji wayarsa na ruri, da sauri ya Kai hannu ya dakko ta ,abin da yaganine ya daga masa hankali miss call kusan 30 Kuma Amma, da sauri ya daga kiran ,kafin yace wani

abun yaji muryar Amma tace "idan ka gama bacci ka fito musu da 'yar mutane muna jiranku a sashen goggo" daga haka ta katse wayar, kirji ya dafa hadi da cewa "innalillahi wa inna ilaihirraju un kardai Amma TA shigo dakinnan, to Amma mai zamuje Yi a part din goggo?" Tama salwa zaro ido ta shigayi Jin yadda ya tada hankalinsa Yana salati.

Babu shiri suhail ya mike ya shiga bathroom tare da wanke miyar da ta bata shi, ya sauya kaya, itama salwa da sauri ta mike kafin ya fito ta fita a guje, bata tsaya a ko ina ba sai a sashen su.

Suhail Yana fitowa bai ganta ba ,Daman yasan za ayi haka, baice komai ba ya fice, daga part din ya nufi da shen goggo.

Acan bangaren salwa Kuwa bayan ta shiga dakinsu, Ihsan ce ta kalleta tace "Kee wai ina kikaje ne aketa nemanki?" "Uhm ke dai bari zan baki labari idan mun dawo daga yaron can" tabe baki Ihsan tayi tace "uhm salwa kenan muje too" dai dai lokacin da salwa TA saka riga Sannan ta dakko dogon hijabi ta zura suka fita.

Falon goggo ya cika da mutanen gidan yanzu Babu wadan da ake jira sai Ihsan da salwa , gefe guda Kuma Big bro ne zaune a kusa da Amma sai watsa masa harara take, gaba kidaya suhail yariga da yasha jinin jikinsa, sallamar salwa da ihsan sukaji hakanne yasa kowanne a cikinsu ya dawo da kallonsa gasu, musamman Abdul da bilal da Umar duk sun bita da ido, ita Kuma tafiya takeyi duk tabi ta tsargu jikinta a sanyaye take tafiya, karasawa tayi kusa da su Abba ta durkusa tace " Abba ina wuni?" Amsawa sukayi gaba dayansu cike da murmushi kowanne a kan fuskarsa sukace "lafiya klau ummiterh , juyawa tayi suma su huzaifa ta gyshesu, suma amsawa sukayi cikin fara,a hadi da kara yabawa da tarbiyya irinta salwa, sukuwa su zubai da tsaki suka ja, Ameera tace "sai kace wata mutuniyar arziki ado Le ita sai ance tafi kowa" Sarai salwa tajira Amma batace mata komai ba.

Abbane yayi gyran murya yace" Kun San kowacce kaddara tana iya sauyawa mai kyau ko mara kyau ,sanan komai da kuka gani ubangiji Yana iya sauya shi, Kuma ance bayan wuya akwai dadi". Tom babban dai abin da yasa muka Tara wanan zama shine Abdul salwa da Kuma suhail, dumm gaban suhail ya fadi haka itama salwa da Abdul kowanne sai zare ido yake Yana Sosa Kai, abbane ya ciga ba da cewa..

"Ada munyi wani tunani game da Abdul ,yadda mukaga tsakaninsa da salwa akwai so da kauna, sabanin suhail da yake nuna ko,in kula akanta, mun yanke shawarar Zamu mai da auren salwa kan Abdul " "what' Abba auren salwa Abdul zaiyi?' to nawa auren da yake kanta fa?" Big bro ya fada a razane batare da sanin maganar ta fito daga bakin saba.

💋 *SALWA* 💋

*©HAFSAT UMAR DANGORO*

Chapter 4

"Ban ban Gane ba wai mai kuke shirin Yi akan haka wannan abu sam bai kamata ba, Indai har suhail zai saki salwa to Babu Wanda yafi dacewa da auren ta irin bilal" cewar yaya babba, zaro ido Umar yayi yace Momy bilal Kuma wallahi Indai bilal ne zai auri salwa sai dai in kowa yarasa ai gwara a barwa ya zaman " haushi da bakinciki ne ya cunkushewa suhail zuciya bai San sanda yayi wata iriyar kara ba yace "ya Isa haka, wannan ai hauka kuke, sai ku bari idan na saketa kwayi fadan akan ta Amma Banda yanzu Abba ka fada musu zan batawa yaro Rai anan gurin" baki Abba ya saki ganin yadda suhail ya gigice lokaci guda yanayinsa ya sauya kamar zai daki mutane, Daman abin da Abba yakeson sani kenan Kuma ya Gane cewa maganar da Amma TA fadamasa gaskiya ne yanzu suhail Yana son salwa..

Zubaida da sauran matan gidan Kuwa bakinciki ne ya ishesu jin yadda suke ta fada akan mace Daya , afili tace "ban da an raina mana hankali muma ai matane sai kuzauna kuna ta fada akan wannan yarinyar wadda Babu abin da ta sani sai kauyanci ,ai kin banza anyi asa....

Bata karasa abin da zata ceba taji wani saukar wawan Mari a kuncinta hagu da dama ji kuke tasss tasss , Abdul ne da Khalid suka tsinketa da mari a lokaci Daya, wani uban ihu ta kurma a razane ta kwasa a guje ta dawo sai da tayi zagaye uku Tana tsalle Tana kuka Sannan ta kwanta a kasa tana ihu "wayyo Allah Momy sun kasheni , shikkenan fuskata tacire wayyo Momy kina ina" da sauri Momy ta taso ta zauna a gabanta Tana cewa "sai na ci abu ta kaza na ubanku Abdul akan wannan 'yar kauyen yarinyar Zaku illatamin tawa,uban mai tayi muku,ai gaskiya ta fada sabi da tsantsar asara Kun nacewa yarinya guda Daya kamar Rai ,wallahi bazan lamunci wannan iskancin ba duk Dan iskan da yasake dakarmin 'ya sainayi shari,a dashi shashashai kawai" itakuwa zubaida Kare makale Momy tayi tana cewa "Momy dubamin sun ciremin fuska ko , shikkenan nasan Babu mai aurena" "Yi hakuri zubaida tashi Babu wan da ya cire miki fuska Tana jikinki kawai zafin marine , ai WALLAHI ko fuskar suka cire miki sai daya acikin su ya aureki marasa tarbiya kawai" ta karasa maganar hade da watsa musu harara.

Uncle Kabir ne yace "to ya Isa haka kuzo ku samu guri kuzauna muyi abin da ya taramu, bana son sha shanci" "tab Allah ya sauwake nakara zama anan huce Nan, so kake idan muka kara zama Yan zu Kuma su kashemin ita Dan wallahi ba a Isa ayi abin magana muki magana ba ATO" "kehh memuna ni kike fadawa haka ni?...ni Kabir kike fadawa haka, to wallahi kika sake kika bar gurinnan abakin aurenki "

"Innalillahi wa inna ilaihirraju un Kabiru yanzu a gaban nawa kuke wannan abin ,wai yaushe zakuyi hankali ku hade kanku,wannan wane irin tashin hankali ne Kun hana yarinya sakat kamar ba jinin kuba, kinga memuna kina rabamin zuri,a saikin bar gidannan" goggo ta fada hadi da watsawa Momy harara,

Uncle faruq ne yace " aini duk abin baikai na fada ba, tun farko Abdul da Khalid Baku kyau taba bai kamata ku Mari zubaida b fada ya kamata kuyi mata Amma ba mariba ,ni banason haka kudaina,yaya ci gaba da magana"

Abbane ya sake kallonsu yace " uhm a gaskiya abin da ya faru yanzu a gurinnan banji dadi ba, kafin ku fara magana kamata yayi ku tsaya na dasa aya zai fi , Amma Baku tsaya na sanar muku dalilin da yasa Za a mai da auren salwa kan Abdul ba kawai Kun soma surutai, bakuji mai nace ba ada munyi tunanin za a maida auren salwa kan Abdul yanzu Kuma Babu wannan maganar an fasa, tun da dai mun fahimci suhail Yana sonta Kuma itama Tana sonshi" wani bakincikine yazo zuciyar suhail ya tsaya Jin yadda Abba yace wai Yana son wannan yarinyar,take yaji haushi yace "Abba yanzu mai ka yanke akai domin zabinka shine nawa ,ina son in koma daki kaina yanamin ciwo"

"Okay abin da na yanke game da auren ka shine, tun da yanzu mun fahimci kuna tsananin bukatar junanku, daganan gurin zaka huce da matarka part dinka domin tarewa" kansane yaji Yana wani irin juyawa bakinsa nason cewa wani abu sai dai Amma ta katseshi da cewa "karka ce komai da idona na ganku kuna bacci ,ko ba kubane?" Zaro ido suhail yayi arazane, hadi da sun kuyar da Kansa kasa, domin Babu yadda ya iya yariga da ya kulle Kansa Kuma Babu mai fitar dashi sai Allah.

Mamey Kuwa salati tayi tana tafa hannu Tana cewa "innalillahi wa inna ilaihirraju un oh yau anyi walkiya ta haska, kana ganinta sumi sumi kamar batasan komai ba Ashe 'yar bari kice, ba a banza ba mazan gidannan suka manne miki ,mebi kin taba basu sun Dan Dana ko, wato sukuma sunji dadi munafukan banza munafukan hofi, Daman andade ana cewa Abdul Yana ruke miki hannu Yana rungumarki Ashe dagaske ne haka kike,yau gashi har bacci kike da suhail a boye, duk da mijinki ne ai ky bari akaiki Shima shahararren Dan iska, sumi sumi dashi Ashe Shima ... " "Keeeh Jamila dakata, bance ki fassaramin 'ya',yaba danace bacci suke wani abun nace miki sunayi ,idan ma wani abun sukayi ai mijin tane" Amma tafada Rai a bace.

Abdul ne ya mike zumbur jijiyoyin Kansa har fitowa sukayi tsabar zafi da zuciyarsa take masa, wani irin jiri yaji Yana shirin kwashesa da sauri ya dafa bangon dakin, numfashin sa ne ya soma fita da sauri dasauri ,lokaci guda ya soma ganin biji_biji take ya yanke jiki ya fadi a gurin, da sauri su Abba sukayi Kansa suna salati, goggo Kuwa kuka tasaka wai za a kashe mata jika, ita kadai sai surfa uwar masifa take..

Uncle faruq ne yayi saurin dagoshi suka hada ido ,yasa hannu ya bubbuga bayansa tare da buda idon sa yace "Abdul kana lafiya ? Mai yasame ka ?"  Wasu zafafan hawayene masu dumi ke zubowa daga cikin idon sa, yama kasa cewa komai sai kallonsu kawai da yake da ido.

A gigice salwa ta karaso gabansa ta durkusa ,tayi zaman sallah hawaye na bin kuncinta,Tana girgizawa Abdul Kai, "ya Abdul Dan Allah katashi kada ka mutu wallahi Yaya ba laifina bane laifin kaddarar muce ,bansan komai ba, Allah shi yabarwa Kansa sani, ubangijinmu baya bacci nasan ayanzu haka Yana ganin halin da muke ciki Dan Allah katashi" "uhm Abdul yayi murmushin takaici yace "meyasa haka Mai yasa salwa? Mai nayi muke Daman kinason yaya suhail,meyasa Zaki cutar da zuciyata a lokacin da aka daura aurenku da yaya, nadamu daga baya Kuma sai na sawa zuciyata dangana, Dana fahimci yaya bakya gabansa hakanne ya Bani kwarin gywa akanki, shine yanzu zakije soyayya tajaki har ku kwanta da yaya, yanzu gaki gashinan ancika miki burinki soyayyar bangare Daya bazata taba yuwuwa ba,dole sai da bangare biyu kanwata" hannu yasa ya goge hawaye ,"yaya Dan Allah kayi hakuri wallahi ni dakaina nayarda yaya suhail baya Sona sabi da shi ba tsarana bane kada kamin mummunan zato wallahi ba laifina bane ka tsaya na Maka bayani" banza Abdul yayi mata hadi da mikewa daga jikin uncle faruq ya taka zuwa dakin goggo,gaba daya mutanen gurin binshi sukayi da kallo,i takuwa mufida cewa tayi" oh jibeshi Dan Allah wai akan mace a kan mace zai kashe Kansa, mudai Allah ya kawo mana sauki da ran gwami.

A fusace suhail ya bar gurin ransa namasa zafi yanajin mamey na kiransa yayi mata banza, shi Kuwa Abba karasawa yayi ya tsuguna tare da dago salwa ya goge mata hawaye yace "kiyi hakuri ummiterh Maza kibi mijinki Allah ya yimiki albarka" Babu musu jiki a sanyaye ta soma tafiya har ta fita daga falon jikinta Babu kwari.

Suma mutanen gurin duk watsewa sukayi kowa ya koma part dinsu, Ihsan ce kurum ta shiga dakin goggo Dan taga halin da Dan uwanta yake ciki.

Tana shiga ta sameshi a kwance idanunsa a lumshe, ya tada Kai da kafar goggo, gefan gadon ta samu ta zauna, hadi da kamo hannun sa ,murya a sanyaye tace

" Ya Abdul!"
A hankula Abdul ya bude idonsa ya saukesu a kan kanwar sa Ihsan , murmushin karfin hali ya sakar mata Sannan yace

"Naam Ihsan"

"Ya Abdul kayi hakuri Dan Allah kada ka sawa kanka damuwa wallahi na kasa samun nutsuwa tun lokacin da Naga ka fadi, Dan Allah Yaya ka kwantar da hankalinka, tun da kaga haka tafaru to ka kaddara salwa ba matarka bace, yaya da wannan tunanin da kake gwara ka tashi ka dauro alwala kayi sallah ka roki ubangijin da ya dasa Maka soyayyar salwa a zuciyar ka akan ya

kawo mana mafita " Ihsan ta karasa maganar tana dan rausayar da Kai.

Kafin Abdul ya bude baki yayi mata magana, sukaji an turo kofa, wace, Ameera ce idanunta sun cicciko da hawaye ,bakin ta har rawa yake wajan karasowa tace"ya Abdul! Dan Allah kada ka kashe min kanka wallahi ni ina sonka Kuma inason rayuwarka , please kada kayiwa rayuwata illa idan katafi kabarni bansan Inda zan saka rayuwa ta ba, ina sonka ka yaya" adda Ameera ta sake fashewa dakuka idanunta na zubda hawaye.

Shi Abdul mai makon ma yaji ta bashi tausayi sai Kuma wani sabon haushinta dayaji ya ziyar Cesa ,wata uwar tsawa ya daka mata yace "shiruu ..... Ni nace miki mutuwa zanyi da zakizo kina karamin ciwan Kai, meyasa baki da hankali ne Ameera ,kinzo kin sani agaba kina kuka kamar Wanda mamey ta mutu, nace bana son ki bana kaunarki kifita' daga rayuwata kinkiji" ya karasa maganar yana huci kamar wani zaki.

"Yaya Allah ina sonka Dan Allah kadaina cewa baka Sona bana jin dadi, rayuwata takace yaya kadaure ka bani zuciyar ka, wanan shine kadai samun masalaha a gidannan domin mamey tace Indai baka aureni ba ya huzaifa bazai taba auren Ihsan ba"

Uhm Abdul yayi wani murmushi mai ciwo sanan yace "idan huzaifa bai auri Ihsan ba zata mutune? Ko mazan duniya sun Kare ne ,Indai sabida 'yar uwata Tana son yayanki za ayimin sarka da haka, to kucire Rai da aurena domin zuciyata ta mutum dayace Kuma na mallakamata ita, fitar min daga daki tun kafin na miki Dan banzan duka a gidannan"

Ihsan dake gefe Kuwa Tana Jin abin da Ameera take cewa ,kuka tasaki ta ja kafafuwanta da ker tabar dakin, bata tsaya a ko ina ba sai a dakin su,bakin gado ta je ta zauna, tare da kallon ko ina na dakin, duk sai taji Babu dadi ,sabi da Babu salwa ,Daman salwa ce mai rarrashin TA to itama yanzu abar rarrashi ce, Kuma an rabata da ita, yun kurawa tayi ta kwanta ,hadi da lumshe idonta tace "lamarin gidannan sai a hankula yanzu ita mamey abin da tace kenan kawai sabi da Abdul bai so Ameera ba, shine Nima zata rabani da farinciki na, bayan ni ba soyayyar bangare Daya nake ba, Yana Sona ina sonshi,haka dai Ihsan ta cigaba da tunane tunane har bacci mai nauyi yayi awan gaba da ita.

°°°°°°'°°°°°°🥺°°°°°°°°°°°°°°°°

Tun da salwa TA karasa sashen Big bro taji dakin a rufe' hatta falon nasa gaba daya ya kullesu, cikin bakinciki da takaici ta samu daidai mattatakalar dake lanbun gidan TA zauna, tagumi ta rafka Tama rasa mai yake mata dadi, cikin bakinciki da zafin abin da suhail yayi mata yasa ta fashe dakuka tana cewa "yaya why ? Mai yasa baka Sona kasakeni mana wan da yake Sona ya aureni " Tana kuka tana surutai ga sauro Yana TA faman cizonta,

Tanan gurin a zaune aka fara wata iska mai karfi da walkiya, lokaci guda hancinta ya toshe ta Soma alamun mura, yayyafi aka somayi can Kuma ruwa mai karfin gaske ya soma sakkowa

kamar da bakin kwrya,har ta mike zata tashi sai Kuma TA koma TA zauna ruwan ya cigaba da dukantanta Tana kuka tana ranar sanyi ,domin ita atunannin ta wannan shine mafita ga rayuwarta gwara ta mutu ta huta inyaso tabi abbanta da ummanta.

💋 *SALWA* 💋

*©HAFSAT UMAR DANGORO*

Chapter 5

Shi Kuwa gogan naku yanacan kan bed a lullube sai dai ya kasa bacci shi kadai yake ta faman juyi a kan bed din, musamman yadda yaji an soma zuwa sai yayi tunanin ai ya rufe' kofa to ina salwa TA shiga, mike wa yayi da sauri kirjinsa na dukan Tara_tara har ya fito daga part din, a gigice ya shiga duba ko ina na part din amma bai ganta ba, runtse ido yayi ya bude hadi da cewa "ya salam wai maiyasa nake hakane?" Furzar da iska yayi tare da juyawa a fusace zai bar gurin, juyawar da zaiyi ya hangota zaune a lanbun gidan a kwance sai karkarwa take Tana wani irin nishi kamar ranta zai fita, zaro ido suhail yayi hadi da cewa

"Innalillahi wa inna ilaihirraju un" ya fada tare da kwasowa a guje ,Yana gudu Shima ruwa na dukan sa har ya karaso in da take, da sauri ya durkusa a kasa tare da tallafo kanta yace "tashi ummiterh ki tashi ,meyasa Zaki zauna ruwa ya dakeki babee? Kuka salwa ta saki hadi da sake rungumo shi tace "yaya ! Yaya sanyi ,sanyi nakeji , cak ya sake tallafota hadi da dannata kirjinsa kamar zai SATA acikin kirjin nasa, kuka tacigaba dayi Tana cewa "yaya Shin Dan Allah dagaske Daman baka Sona, kake azaftar Dani haka" shiru yayi mata batare da yace komai ba, ya dagota gaba daya zuwa kirjinsa tayadda Yana iya jiyo sautin fitar numfashin ta itama tanajin nasa.

Tafiya ya somayi har ya Isa falon sa, Kai tsaye akan kujerar ya ajiyeta, Ganin yadda take rawar sanyine yasa ya kama hijabin dake jikinta ya cire, a take yaji wani abu ya fizgeshi Jin ganin yadda rigar ta manne a jikinta, sakamakon ruwan da ya daketa, runtse ido yayi tare da budesu a kan kekkewar fuskarta yayi ,sai da yakai kusan minti 5 Yana kallonta Yakasa dauke idonsa a kanta can Kuma sai ya mike , bedroom ya shiga ya dakko rigarsa fara jallabiya ya Mika mata, Kar ba tayi, ta tsaya tana kallonsa ko zai tashi ,ina bai masan Tana yiba, wata uwar harara ta watsa masa Sannan tace" Yaya ka tashi zan canza rigar" banza yayi mata baice komai ba Kuma bai tashi ba, saima kara gyra zama da yayi ,ya cigaba da Danna waya,

Sun kuyar da kanta tayi tare da rabawa ta gefansa ta huce bathroom ,shikuwa gogon namu bin bayanta yayi da kallo hadi da yin kwafa yace "saina gyra maki zama wato na tashi ko, bazan tashi din ba sai dai karki cire uban mai zan gani a jikin naki" ya karasa maganar hadi da yin tsaki.

Salwa tana shiga bathroom ta rasa mai zatayi sabi da takaici, sai kawai ta shiga cikin kwamin wankan ta fashe da kuka, tare da takurewa guri Daya, sai da salwa tayi mai isarta Sannan tayi wanka ,ta zura jallabiyar ,sai gata tayi zulun_zulum aciki Inda kasan a nannadeta haka tayi mata yawa, diban kayan da ta cire tayi ta ratayesu Sannan ta kara tsayawa a cikin bathroom din ta kurawa kofa ido Tana ta tunani,ko tunanin mai take oho

Shiru_shiru suhail Yana falo Yana jiran fitowarta Amma sai yaji shiru, Nan take yashiga zagaye falon Yana tunanin ko dai yarinyar Nan ta mutune, kasa jure hakan yayi ya koma bedroom ya dakko zanin gado karami mai Dan kauri, ya fito, bathroom run din ya nufa, can Kuma sai ya tsaya a bakin ban dakin Yana tunanin, kamar ya shiga kamar Kar ya shiga ,Kar yaje yagano abin da yafi karfinsa,wata zuciyar Kuma tace "to saime idan kashiga ai matarkace tasunna, ya halatta kaga komai, kafada big bro ya dage hadi da tabe baki ya tura kofar, a razane salwa TA dago suka hada ido ,cike da mamaki yake kallonta, itama kallon nasa take cikin takaici, can Kuma sai ta fashe da kuka mai karfi ,har da kwanciya a bathroom din Tana kuka, haushi da takaicine ya tsaya a zuciyar suhail,bai San Lokacin da ya daka mata tsawa yace "yimin shiruu.... Uban mai nayi miki kalla yadda kika batamin riga daga baki ki saka shine har kika kwanta acikin bathroom haka, baki da hankali to wallahi sai kin wanke min, tashi Maza" ya daka mata tsawa, ai da sauri salwa ta mike Tana zazzare ido har da 'yar kwalliyar ta a ido , baki ta tabe tace "tsakani da Allah Yaya baka kyauta min ba yanzu da ace bakaya a jikina fa, shine zaka wani shigo Kai tsaye" "wai ke wane ya koyamiki wannan 'yar iskar shagwabar duk anbi an bata ki, kafin a aura miki ni ba a ce miki kinzama mallakina ba, to ma wai ,mai zan gani a jikinnan naki kamar kaza aba kamar na hureta" ya karasa maganar hadi da janyo tawul ya ajiye a gefe Sannan ya kamo salwa, suka tsaya face da juna, hannun sa ya Kai kan wuyan ta ya shiga balle maballin rigar Sannan ya saka hannu ya daga rigar cak ya cireta, wata uwar kara salwa ta daka hada fadawa kirjinsa tayi mutuwar tsaye, abin da bata sani ba tun tuni suhail ya runtse idonsa Dan Shima bayason wani abun yashiga tsakanin su, Amma sai Kai fadawa jikinsa da tai ta rungume shi yayi sanadiyyar dauke war numfashinsa na Dan lokaci ,can Kuma ya Yi kokarin saita Kansa, da sauri ya dauki tawuldin ya lulluba mata, ya fice, sake zama salwa TA karayi a gurin zaman dirshan tace "na shiga uku Daman yaya 'dan iskane?" Runtse ido ta sakeyi Sannan ta saki wata ajiyar zuciya ta mike, ta daki jallabiyar ta SATA a ruwa ta wanke, Sannan ta

sakeyin wanka ta daura wani tawul din ta fice.

Lokacin da ta fita bata sameshi a faloba hakan yasa tayi tunanin Yana bedroom ya kwanta, Dan haka itama ta nemi guri a falon ta kwanta sanyin AC na sake dukanta ahaka bacci ya dauketa badan tanajin dadin yin baccin ba.

Shiru_shuru suhail ya na kwance Amma baiga salwa tashigo ba, abin ya bashi mamaki ,da yayi tunanin ko ya kwanta yayi baccin sa, Amma sai ya kasa sabi da tunanin halin da take ciki, tsaki yayi ya duro daga kan bed din ,ya kunna kawai ,daga shi sai gajeran wando, fitowa yayi falon ya na nemanta hatta bathroom sai da ya duba bai ganta ba, abin ba karamin bashi mamaki yayi ba, a hankula ya furta "to ina yarinyar Nan ta shiga?" Juyawar da zaiyi ya hangota kwance a kan 3 star sai baccin ta take Tana sauke ajiyar zuciya, tsayawa yayi cak a gurin ya tsuramata ido Yana kallonta zuciyarsa a chunkushe, tsaki yayi ya karasa kusa da ita ya zauna, yayi tagumi Yana tunani, "Anya Anya kuwa gaskiya da sake ,ni bazan iya zama da yarinyar Nan ba ,haba Abba ya zakai min haka" shi kadai dai ya cigaba da durutansa Yana kallonta,can Kuma yaji bacci mai nauyi ya soma kamashi,babu shiri Big bro ya mike ya saka hannu ya dauketa chak kamar 'yar baby, bai ajiyeta a ko ina ba sai kan bed, bargo ya janyo ya rufa mata Sannan Shima ya kwanta a bayanta bacci mai nauyi yayi awan gaba da su.

...............

A bangaren Abdul Kuwa yadda yaga dare haka yaga safi,domin kwana yayi Yana tunani yasaka wancan ya warware wannan, abin duniya ya hadu duk yayi masa yawa, ciwan son salwa Yana son ya sashi a masifa, shi kadai sai surutai yake Yana cewa "yanzu shikkenan narasa salwa har abada' bansan yazanyi ba, ni inan kamar zan mutu sukuma sunacan Babu abin da ya damesu,mebima soyayyarsu kawai suke Sha, Anya zan iya cire soyayyar ummiterh a zuciyata ,wai meyasa hakane ,meyasa zuciyata zata na rayamin wani abu akan Dan ,uwana Kai Anya kuwa, to kodai na kashe big bro in yaso sai ni na aureta, Kai gaskiya bazan iya kashe shi ba yaya suhail ba ko wanine yace Yana son salwa bazan iya kasheshi ba, balle Kuma d'an ,uwana kash na nemi wata mafitar dai" haka dai Abdul yayi ta sake sakensa Yana surutai a haka har gari ya waye ko runtsawa bai ba, Banda bacci marawo dayiyi awan gaba dashi.

💋 *SALWA* 💋

*©HAFSAT UMAR DANGORO*

Chapter 6

========IN THE MORNING========

Da sassafe su adda zubaida da dasauran 'yan matan gidan suka zo lambu suka zauna tsabar gulma da munafirci , sakamakon wanna lanbun a bakin kofar part din big bro yake,

Shiru_ shiru suna zaune a part din goggo ko zasuga shigowar su salwa ,Amma ina sai sukaji shiru hakan yasa suka dawo lambu domin su kashe kwarkwatar idonsu, sai dai zuwansu bai karamisu komai ba sai haushi da takaici, mufida ce ta kalli zarah tace "iyee wai uban mai sukayi haryanzu shiru basu fito ba, ni fa nayi tunanin zanga shegiya a harabar Nan a yashe Amma Kuma naji shiru" dariya Ameera tayi tace "ai dole kuji shiru jiya sun kwana basuyi bacci ba ,idan ma Zaku daina jira kudai na ni kunga tafiya ta" ta mike tare da yin hanyar part dinsu,harara zubaida ta watsa mata tace "to uban mai suke Harda zasu kwana basuyi bacci ba? Kinsan dai Babu abin da zaici da wanan kwailar" dariya zarah tayi tace "au Amma dai itama macece ko,mai zasuyi idan Banda soyayya, Nima bazan iya jiran wanan takaicin ba, itama ta mike tayi wayi cikin gidansu, kuka zubai da ta saka hadi dacewa "wallahi ni Daman nasan ni kadai nakeson yaya suhail tsakani da Allah gashinan duk baku damu ba akan abin da akayi Mana', wallahi saidai idan yarinyar Nan bazata fito ba Amma saina koya mata hankali..... Haka dai zubaida tacigaba da masifarta tabar gurin..

Tun da salwa TA tashi ta juya ta ganta a kan bed kusa da suhail,hankalin ta ya tashi, runtse ido tayi ta bude tare da saka hannu ta goge idonta domin ta faeka idan ma mafarki take, aikuwa tana budewa still dai akan gadon ta ganta, tagumi ta rafka tare da kurawa fuskar big bro ido, azuciyarta Kuma tace "ni dai nasan da kafata ban shigo dakin Nan ba afalo nazauna har bacci ya daukeni, to Amma abin tambayar shine waye ya kawoni dakinnan ,ko dai yayana, sake kura masa ido tayi tagsnshi baccin sa kawai yake Babu abin da ya sameshi hankalinsa kwance, hakan yasa ranta ya baci ,wato ma ita tana zaune tanajin yunwa shikuma Yana kwance ya saki baki Yana bacci ,to kenan ya zanyi na tasheshi ne?" Tayi tambayar a zuciyar ta, "to kodai cizan sa zanyi ne, a,ah na muntsineshi zafi tashi da sauri ,wata zuciyar Kuma tace "ki samu daidai lips dinsa ki gasa masa cizo zai mike" aikuwa salwa ta jijjiga Kai hadi dayin dariya ta shiga matsawa kusa dashi, sai da taje dai dai kusa da fuskarsa Sannan ta tsaya hadi da durkusawa dai dai kan d'an karamin bakinsa Sannan ta dora nata bakin a kan nasa ta cafki lips dinsa na kasa, ta gantsara masa cizo, A furgice suhail ya bude ido hadi da kurma ihu yace, "wayyo Allah na Amma!!!!!!!! .........." A razane salwa TA daga shi, ta koma gefe ta takure guri Daya, tana zare ido ,itace ta cijeshi Kuma itace dayin kuka, Harda rawar sanyi duk tabi ta burkice sabi da tsoron abin da zai mata,

Shikuwa Yana gama ihun ya mike tare da karasawa gaban mudubi ya kurawa bakinsa ido yadda yaga ya kunbura yayi zumburbur ,runtse ido yayi sabi da tsabar takaici Yana tunanin abin da zaiyiwa wannan yarinyar ya huce , can Kuma sai ya hau kan gadon kan gadon Rai a hade kamar Daren mutuwa fuskannan, karasawa yayi kusa da ita, hadi da kama hannayeta duk biyun ya danne a jikin bangon Sannan yace "ni sa ankine, Daman haka kike bakina kikeso ko, shikikeson Kisha, hawaye ne suka soma zuba daga cikin idon salwa tana kuka tana girgiza masa Kai alamar ita ba haka take nufiba Amma ina sai ya sake cewa" uhm ni Daman nasani ragowar 'yan kauye aka auramin wato kenan abin da aka fada game da ke agidannan gaskiya ne kina bin Maza" gaba daya salwa ta tattaro dukkan kwarin gywarta tace "wallahi Yaya ba haka nake ba Dan Allah ka saurareni wallahi ni bana bin Maza" tasake fashewa da kuka, "yimin shiruu... "Ya dakamata tsawa Nan take Tasha jinin jikinta tayi kumm., A,C ce ke har bawa a dakin Amma ita salwa gumi take tsabar tsorata da lamarin yayana nata, bata Ankara ba, taji ya hade bakinta da nashi, lokacin guda yashiga tsotsar bakin dakarfi, Yana datsa labbanta da hakoransa, sai da sukayi kusan minti 10 a haka Yana azaftar da ita Sannan ya daketa, baki takeson ta bude tayi kuka ko zata samu sallama Amma ina takasa kukan ganin yadda bakin yake zubar da jini, sosai yadda yaga tanayi ta bashi tausayi Amma sai yaki rarrashinta sabi da ya koya mata hankali Dan bayason raini, fuuuu ya mike ya nufi falon ya zauna, tagumi ya rafka Yana tunani soyake ya fita Amma ya kasa sabi da kumburar da bakinsa yayi ,bayason ya fita ayi zargin wani abun ko ayi masa dariya, tunowa yayi Tanada facemask idan ya rufe fuskar Babu Wanda zai Gane mai ya faru.

Haka Kuwa akai bayan ya Yi wanka ne ya shirya tsaf ko kallon salwa baiba ya saka fecemask ya fice, itakuwa salwa bargo ta janyo domin ta kasa tashi zazzabi mai zafi ya lullubeta ita kadai sai rawar sanyi take abin tausayi,gashi koyaya ta rufe' bakinta zafi takeji, hakadai tai ta kwance adaki ko motsi daker sabi da zazzabi.

Shi Kuwa gogan namu ya na fita part din Amma ya nufa ,a zaune ya samesu a falon ita da Abba, suna Shira, baki Abba da Amma suka saki cike da mamaki suna kallon suhail,Amma ce TA kasa jurewa tace "to yau Kuma fuskarce ba a so mugani kamar wata sabuwar amarya, ni abin naka kara gaba yake Anya Anya suhail, murmushi Abba yayi yace "ai ba karya kikayi' ba hajjaju sabon angone mudinma kunyarmu yakeji " shi dai suhail baice komai ba Kuma bai cire facemask dinba ,sai ma sun kuyar dakai da yayi ,ya tsuguna yace "am Abba barka da safiya Kun tashi lpy" "eyyee lallai ma yaronan yanzunne safiya?" Amma tayi tambayar hadi da zuba masa ido, Sosa keya yashiga ya yace" am uhm  Abba bari naje na dawo" daga haka ya mike da sauri ya fice Yana Jin Abba nacewa "Oh jibi yaro wai Shima yayi amarya' duk ya rude" .

Suhail Yana fita ya sauke ajiyar zuciya yanufi part din goggo, Yana tafe a hanyar harabar ya hadu da ihsan zata huce da sauri yace "ke ina zakije?" Yiyi maganar tare da tamke fuska, Sosa Kai tashiga Yi tace "yaya ina wuni?" "Lafiya kalau " "Daman zanje gurin aunty salwa ne najita shiru bata fito ba" "to ina ruwanki da rashin fitowar ta ,banason gulma huce ki koma Inda kika fito, ko dawasa naji kinshigar min daki saina kakkaryaki a gidannan" yayi gaba ya watsa mata harara, itakuwa Ihsan sakar baki tayi hadi da bin bayansa da kallo har ya fice, tsayawa ta danyi a gurin tayi shiru can Kuma sai ta juya ta nufi Dakin ta.

💋 *SALWA* 💋

*©HAFSAT UMAR DANGORO*

Chapter 7

Suhail Yana shiga part din goggo dukkan Yan matan dake zaune a falon suka zubo masa ido suna kallonsa, shikuwa bai bi takansu ba ya huce dakin goggo ,yanaji suna gaishesa Amma bai kulasu ba ya huce, zarace ta dawo kusa da mamey ta zauna tace "lallaima gayennan wato ku bukukai ya gaysheku ba sai kace wan da yaga sa,arsa"kwafa mamey tayi tace kekuwa jiya na zagi 'yar gold ta ina zai kulani ai bazai gaisheni ba, tun da ubansa na zaga, uhm jibifa Mamey har da wani sako facemask kamar wani munafiki sai kace bamusan asalin fuskar ba" cewar mufida, uhm ku kuka damu dakuga fuskarsa kuka sani ko ita salwan ce ta hanashi fitowa a haka sabida kada a kalar mata fuskar miji" cewar adda Ameera " tsaki zubai da tayi tace uhm wato fuskar tashi ma damuke kallon muna Jin dadi tasa yarufe ta , wallahi sai mun tashi tsaye, dan yarinyar nan na fahimci ta gama mallake ziciyar yaya suhail.

Tom suhail na shiga dakin goggo yaji zuciyarsa ta wani buga da karfi jikinsa lokaci guda yayi sanyi ,a hankula ya shiga Jan kafafuwansa har ya karasa bakin gadon ,kafesa da ido yayi Yana kallonsa zuciyarsa cike fall da tausayin sa... Gefen gadon yasamu ya zauna kusa dashi, hannun

sa ya kama yaruke gam Sannan yace "Abdul ! Kallonsa Abdul yayi daker yake daganinsa sabi da junwa GA jiri duk yafita a hayyacinsa, "Naam yaya,ina kwana?" "Abdul mai yake damunka haka, haba kanina tukunna ma kaci abinci?" Girgiza Kai kawai Abdul yayi batare da yace komai ba ya mai da idonsa kasa, "uhm Abdul bazaka min magana ba? ni nake Maka magana kake min shiru?" Still dai Abdul baice wani abunba yayi shiru ,gajiya suhail yayi da zama Dan yaji shiru goggon bata shigo ba ,Dan haka ya mike tsam ya bar dakin.

Kai tsaye Bai huce part din saba balle yabi takan salwa, mota ya shiga kawai ya fice, sai da yayi tafiya mai nisa, Sannan ya tsaya gefan titi, ya durkusa Kansa a kan sitiyarin motar,shiru yayi yama rasa mai yake masa dadi a duniyar, "Kai Anya kuwa" ya fada hadi da saka hannu ya bude murfin motar ya fito, zagaye gurin yashiga Yi Yana tunani ,yayi Nan yayi can abin duniya duk ya ishesa, "Anya kuwa d'an uwana yanacan kwance duk sabi Dani? To Amma ni mai zanyi da wannan yarinyar in saketa mana ,Kai idan Kuma nayi haka banyi adalciba ita batace na saketa ba saini zan saketa ,bayan nasan Nima bajin dadin zama take Dani ba, to Amma idan ban saketa ba taya zamanmu zaiyuwu bayan ni bason ta nakeba,? A,ah fa to idan ba Santa nakeba menake ,meyasa zan dinga kishi a kanta, ? Kai Anya ba kishi bane tausayinta kawai nake, babban taimakon da zanyiwa ummiterh kawai na sauwake mata kowa ya huta, to Amma Anya su Abba zasu yarda?" Shiru yayi ya dan jingina da jikin motar ,,Sannan ya koma cikin motar ,kunna motar yayi kana ya soma tafiya ya dauki hanyar da Zata sadashi da gidansu. Yana Isa gidan yayi parking ya fito, part dinsa Kai tsaye ya nufa , still dai a kwance yadda ya barta haka take, karasawa yayi kusa da ita yace "tashi?" Banza Tayi Masa batare da tace komai ba, tsawa ya da kamata yace "nace ki tashi muyi magana ko?' da sauri salwa ta mike hadi da sun kuyar da kanta tace "Allah ya baka hakuri yaya ina jinka" "uhm yayi kwafa Yana kallonta can Kuma sai yace "ummiterh! Lokaci guda salwa taji kirjinta ya buga, jikinta yayi sanyi tarasa dalilin Jin haka, Amma sai ta daure tace

"Na am yaya!"

"Na fahimci zamana dake bazai taba yuwuwa ba domin ni inason zama da wadda zan iya soyaya da ita Kuma wadda nake so take Sona, so Amma ke ina kallonki a matsayin kanwata Kuma yarinya karama bana son raini bazan iya zaman aure da keba ,kiyi hakuri kinji bawai nakasa cikawa Abba muradinsa ba no kawai dai nafahimci ina cutar dake haka Nima kina cutar da ni ,ki tashi kisaka hijabinki mutafi, kiyi gaba ganinan zuwa kicewa Amma duk Akira kowa inason a shaida da wanan abin kinji" hawayene masu zafi suka soma fita daga cikin idon salwa, bakinta na rawa tace "yaya rabuwa zakai Dani?" Banza yayi mata baice komai ba ,saima cewa dayayi "kitashi kiyi abin da na sakaki" salwa bata sake cewa wani abin ba ta mike tsaye jiri na dibanta ta dafa bango ta dakko hijab ,bayan tasaka ne ta soma tafiya jinin duk ya bushe mata a lips sabi sabi da azabar da yayi mata dazu, a haka ta daddafa bango tasoma tafiya har tafita daga part din sa.

Tana cikin tafiya a hanya taci Karo da ihsan zata fita, da sauri salwa tace "Ihsan " gamamakin Ihsan taju Tana kallon salwa, yanayin yadda tagantane hankalinta ya tashi, cike da tausayin ta takaraso kusa da ita ,hadi da kama hannun ta tace "nashiga uku salwa mai yasami bakinki haka ,ina zakije Kuma?" Tayi maganar Tana kallon salwa, itakuwa salwa hawayen da take boyewa ne yashiga sakkowa, zuciyarta tashiga bugu lokaci guda, kawai ta fada kirjin Ihsan tasaki kuka mai ban tausayi, hankalin Ihsan ne yatashi Tama rasa mai zatace ,can Kuma sai tace "salwa wai Maine yafaru kodai yayane wani abu ya sameshi? To ko sakinki yayi?" Kukan da salwa take ne ya daina fitowa sai dai kukan zuci ,daga karshe Kuma tace" Ihsan ina zakije?" "Uhm inason zan fita ne ?" Indai ba abune mai mahimmanci zakije ki ba gwara ki zauna domin yaya yace Yana bukatar ganin kowa a babban falo" "to falo Kuma mai yafaru lafiya kuwa Anya?" Uhm uhm nashiga uku Ihsan wallahi ni kaina bansani ba ,mebi lokacin mutuwa tane yazo bansani ba,Allah nagaji da rayuwar wanan duniyar natsani kaina" "kiyi hakuri kinji ummiterh komai yayi zafi maganin sa Allah yanzu ina zakije to ansanarwa da kowa?" "A,ah yanzu yace naje na sanarwa da mutanen gidannan harsu uncle" "okay kije Maza kizauna a falon ni bari na kirasu. Daga haka Ihsan ta bar wurin, Tama salwa TA karasa sashen goggo.

Kai tsaye bangaren mahaifanta ta nufa ,ta sanarwa da su Amma, gaba daya hankalinsu ya tashi hatta Abba Saida yaji gabansa ya fadi daganan ya yanke shawarar ya kira sauran 'yan uwansa a waya idan ma basa kusa duk su dawo gida, haka Kuwa akai kowa aka sanar masa gaba dayansu duk suka cika da mamakin Maine dalilin hada taronnan,hatta Abdul sai da aka tasoshi ya lallaba ya fito ya zauna, su Kuwa Daman iyayen gulma su ameera sun dade da dura a falon Dan dama kwanciyace kawai take rabasu da zaman falonnan,  kowafa na gidan ya hallara mutum daya ake jira Big bro, salwa Kuwa na gefen Amma ta dukunkune a jikinta sai tunani take tana faman kukan zuci.

Yanzu kam big bro bai saka facemask dinba sabi da bakin nasa ya sabe, fuskan Nan tasa a hade kamar daran mutuwa, duk da hade ran dayayi kyen fuskarsa bai fasa bayyana ba, domin shi suhail ko mai zaiyi sai kinga yayi muki kyau, musamman ma Yana dariya dimple dinsa na lotsawa, zama yayi  a gabansu Sannan ya gaishesu, amsawa sukayi Sannan suka zuba masa ido suna kallonsa, kasa cewa komai yayi Dan haka ya sinnar da kansa kasa baice uffan ba, abbane ya kalleshi yace ...

"To ubbanmu gamu mun hadu Kai muke jira"

Dagowa yayi hadi da Sosa Kai Yana kallonsu Daya bayan Daya can Kuma sai yace "am uhm Daman Abba uhm ina son na sauwakewa ummiterh ne" daram gaban mutanen dake gurin

ya fadi musamman Amma da Abba da sauran su uncle, zaro ido isana tayi tace "saki?" Ita Kuwa salwa zumbur ta mike hadi da kuramasa ido Tana kallonsa,

Uncle faruq ne yayi kokari ya tattaro duka karfin halin da yake dashi a lokacin yace" saki fa BABANA mai yafaru idan Rai ya baci ai hankali bai kamata ya gusheba... Saurin dagawa uncle hannu yayi yace " ya Isa haka kubarshi yafadi abin da yakeso ayanzu ni kan na tabbat ban Isa da suhail ba cigaba damaganar ka "

Shiru yayi Ihsan kuwa ta dawo gabansa hadi da kama hannun sa tace "Dan Allah Yaya kada Kai haka wallahi salwa Tana sonka, kamanta da amanar da uncle ya baka maiyasame Kane yayana,kada kyen dakake da shi da jiji dakai yasa ka manta da wacece salwa a wajenka....

💋 *SALWA* 💋

*©HAFSAT UMAR DANGORO*

Chapter 8

Tsawa ya daka mata yace yimin shiruu... A kan mai bana son auren nan natsani yarinyar Nan bazan iya zaman aure da ummiterh ba" "a,ah yaya kada Kai abin da zaka zo kana Dana sani?" No Ihsan akan wanna zanyi Dana sani? To Indai hakane Allah ya tsine wa danasanin " juyawa yayi ya kalle ta tare da Mika mata takarda yace " karbi"..... Dumm gaban salwa ya yanke ya fadi, zuciyarta tashiga bugu lokaci guda hannunta na rawa ta Mika hannu zata amsa idanunta na zubar da hawaye ,saurin dakatar dashi uncle Kabir yayi yace "dakata suhail anya kana cikin hayyacinka Kuwa ,salwa zaka saka ? Suhail kayi tunani akan haka kada ka aikata abin da zakazo kana danasani akai " " no Abba nagaji da aurenan bazan iya zama da yarinyar Nan ba tamin kankanta nafi karfin nayi RAYUWAR aure da ita ... Tasss yaji saukar Mari a fuskarsa abbane ,abin da tun da yake ba a taba masa ba ,yau sai gashi akan ummiterh an mareshi AI yazama dolema ya rabu da ita ko itace autar mata, saurin rike hannun Abba uncle faruq yayi yace "kayi hakuri yaya please ku barshi badai ummiterh ce baya Soba ,ni da hannuna zan amshi takardar sakin da yayi mata, Amma yasani Bama magana biyu zan kara bashi zabi akan haka yaje yayi tunani zuwa Nan da gobe... " Ai uncle bai rufe baki ba yaji Amma tace " Babu wata dama daza a sake bashi, ku rabu dashi Indai wannan auren ne an rabu, Kuma kamar yadda ya rabu da salwa ya rabu da ita har abada' Babu kome"

Abbane ya karbe da cewa "suhail danane Kuma Wanda na Haifa da cikina ,ada nayi tunanin duk abin da mukeso ko bayaso zai hakura ya amshi abin hannu bibbuyu, Ashe ba haka bane" kallon suhail yayi yace "bani takardar ai ba ummiterh ya kamata ka bawa ba tun da ba ita ta daurawa kanta aure ba mune ,Dan haka mu iyayenta muzaka bawa" suhail Kuwa gaba daya jikinsa rawa yake hankalinsa inyayi dubu ya tashi bai taba sanin haka saki yake daciwo ba sai yau, shiyayi tunanin abin kamar wasan yarane jiyake kamar ya fasa ya mai da takardar Amma ina bakin alkalami yariga ya bushe, jiki Babu kwari ya mikawa abbansa takardar sakin salwa, Sannan Abba yace "ku shaida daga yau Babu Suhail Babu salwa har abada' Kuma narantse da Allah ko da suhail zai mutu bazan maida salwa gidansa ba ko bayan Babu raina ban amince salwa TA koma gidan suhail ba, Kuma ku shaida na saka ranar auren Abdul da salwa Nan da shekara 3 kafin Sannan salwa ta Kammala karatunta" kuka salwa ta saki hadi da dukawa a gaban suhail tana kuka kamar ranta zai fita tace "yaya yaya!! Yaya mai nayi maka zakayimin wannan babban hukunci ,yaya ina sonka meyasa kakeson kasheni lokacina baiba ,wayyo Allah na Amma zan mutu.....

Salwa ta sulale a gurin ko motsi batayi, cikin tashin hankali suhail yashiga jijjigata hankalinsa a tashe hannayensa ya zura zai tallafota ya dagata Abba ya daka masa tsawa yace "dakata suhail... Ayanzu salwa ba matarka bace Babu Kai Babu ita !" "Kallon Abba yayi kamar zaiyi kuka yace "Abba ummiterh zata mutu " to saime ina ruwanka da mutuwarta ,da wayaja hakan tafaru ,Kai Abdul Maza futomin da mota, ke Kuma Ihsan khaleesat ku kama salwa ku fitomin da ita, Kai Kuma suhail ko a harabar asbitin na ganka ban yafe maka ba" Abba ya fita a fusace, suma su zubaida mikewa sukayi sukabar gurin domin yau sunga gulma Babu SA,a acikinta Ameera Kuwa Inda kasan zatayi hauka.

Aguje tanufi part dinsu ta fashe dakuka tare da fadawa kan bed, sukuwa ragowar 'yan uwanta biyo bayanta sukayi har dakin suna bata hakuri, musamman zubaida da yanzu hankalinta ya kwanta suhail ya saki salwa ,kallon Ameera tayi ta dafata tace "Dan Allah Ameera kiyi hakuri komai kikaga yafaru akwai sila ki kwantar da hankalinki kiyi hakuri haba sai kace Abdul shine autan maza" "Dalla malama dakata min ke uban Maine bakiba akan yaya suhail duk haukana na kaiku, malama tashi ku fitar min daga daki" Ameera ta fada idanunta na zubda hawaye. Sum sum su zubai da suka mike domin yau dinnan Ameera ta basu tsoro .

Acan bangaren su zaman Kuwa ,gaba dayansu suna zaune a falon bilal , kowanne ya zabga tagumi da tunanin da yake, Umar ne ya soma magana yace "ni Kuwa Anya big bro Kansa Daya Kuwa? Haba jibi fa yadda ya tozarta yarinyar Nan agaban su ameera ,Daman ya akaciki balle yanzu, gaskiya abin da yaya suhail yayi bai kyau taba ko kadan " "uhm ya Umar kenan ni kasan mai Bama Taron dayasa akayi ne ya tsayamin araiba yadda su Abba suke cewa yaje yayi tunani akan haka Yana wani cijewa shi adole baya sonta kamar Wanda akayi masa dole, to shi an fada masa rasa mijin aure tayi Naga dukkanmu Sonta muke shine zaina wulakanta ta, wallahi ina jiye masa ranar nadama" cewar Khalid,shikuwa bilal cewa yayi ...

"Uhm ku wai mai kuke tunani game da big bro? Nufinku wai baya son ummiterh?" ",eh mana yaya baya sonta haka muke tunani" "lallai har yanzu ku yarane, big bro Yana son salwa domin shi Kuwa yakeyiwa salwa soyayyar da mu Bama Yi mata, ina da tabbacin Big bro bai taba soyayya bane shiyasa har yanzu bai San mainene soba,shi Kansa bai San yanason ummiterh ba, ya tabka babban kuskure da yasaki salwa, wannan abin da yayi sai ya hanasa rayuwa mai dadi ,Kuma lokacin da zai sauke girman Kansa da takama, salwa ta masa nisa batajin kira, babban abin da zai bashi matsala a Nan gaba shine uncle LAMI'DO ,Dan Abba kaifi dayane baya yafiya Kuma baya magana biyu, gashi yayi rantauwa bazai mayar da auren ba, Inda zaku San big bro Yana son salwa, lokacin da ta fadi kukalli yanayinsa duk ya fita a hayyacinka, to wannan ma somin tabine" cewar ya bilal ,shiru sukayi dukkan su suna nazarin maganar bilal, can Kuma sai zaman yace tabbas yaya suhail ya debowa Kansa abin da yafi karfinsa, yanzu GA irinta Nan Abba ya damkawa Abdul salwa , uhm Allah ya kyauta kawai.

💋 *SALWA* 💋

*©HAFSAT UMAR DANGORO*

Chapter 9

Tom ana saka salwa a mota abbane da Kansa ya shiga gidan gaba, ya Soma tuki sai Amma da uncle faruq dake zaune a baya shikuma uncle Kabir Yana zaune a gefen Abba, suka nufi asbiti, sai da sukayi tafiya mai nisa Sannan, suka Isa babban asbitin dake cikin garin TARABA, sunayin parking, nurse suka fito da sauri dauke da gadon mara lafiya, salwa aka fito da ita aka sanyata agadon, Sannan suka shiga da ita, Kai tsaye emergency room aka shiga da salwa, sukuwa su Abba suna tsaye a harabar dakin, sai kaiwa da komawa sukeyi,gaba ki Daya hankalinsu a tashe.

Daya daga cikin doctor din asbitin ne ya fito daga cikin dakin, da sauri su Abba suka karasa gareshi hadi da cewa "doctor! Doctor!! Ya jikin nata ,ta farka?" Sukayi tambayar cikin tashin hankali,

Murmushi doctor yayi yace " am uhm Karku damu Babu abin da ya sameta, kunyi BABBAR dabara da kuka kawota ta asbiti da wuri,yanzu dai kawai tsorata tayi GA damuwa da take ciki, inason ka biyoni zan Maka bayani" doctor yayi maganar Yana kallon Abba.

Bin bayansa Abba yayi har suka Isa zuwa office din doctor, bayan sun shiga zama doctor yayi sannan Shima Abba ya zauna, sai da suka dauki kusan minti 2 sanan doctor yaja dogon numfashi ya kalli Abba yace " am yallabai,ka kwantar da hankalinka ba wani abune ya faru da yarinyar ku ba, kawai dai furgicine dakuma damuwa da Tayi mata yawa   ,inason Dan Allah ku kula da duk wani al,amarinta so a halin yanzu depression din bai yawa ba ,idan ma akwai wani abu da kuke mata bata so ,yakamata ku daina tun kafin damuwa tayi mata yawa har yazo ta kamu da ciwan zuciya, idan da dama kuyi kokarin kirkirar mata farinciki tayadda zata na mantawa da abin da ke damunta" shiru Abba yayi daga bisani Kuma yace" nagode sosai doctor in Sha Allah Zamu kiyaye akan haka, yanzu ina son ganinta zan iya?" "Ah ai Babu komai Zaku iya tafiyama zuwa anjima idan ta Dan huta, yanzu kushiga sai ku ganta kafin anjima sai ku huce" okay Abba ya fada sannan yayi doctor godiya har da yimasa kyautar kudade masu yawa, sosai doctor Shima yayiwa Abba godiya ,daganan Kuma Abba ya fita zuwa gurin su uncle Kabir.

Yana zuwa yayi musu bayanin da doctor yayi masa akan salwa, sosai suka shiga damuwa dajin haka Amma sai uncle faruq yace " yanzu  yaya abin da Yakamata muyi shine mukoma gida muzauna akan wanan lamarin domin musamu mafita akai ,Dan Indai har munasan ummiterh ta bar damuwa akan suhail dolene mu ni Santa su d'akuna" girgiza Kai Abba yayi alamar gamsuwa da shawar da uncle faruq ya kawo, "yanzu dai mushiga muga yanayin jikin mata" cewar Amma.

Shiga sukayi dakin bakinsu dauke da sallama, salwa na kwance a kan gadon idanta a lumshe kamar mai bacci, Amma ce ta soma Isa bakin gadon ta zauna hadi da kamo hannun ta tace "sannu salwa" a hankula salwa tashiga bude idonta a kansu Tana kallonsu Daya bayan daya kamar yau ta soma ganin su, Amma ta kalla kamar zatayi kuka tace "Amma ina yayana? Baizo ba ko, shin dagaske yaya baya Sona ya sakeni?"

Shiru Amma tayi tare da sun kuyar da kanta domin Tama rasa abin da zatacewa salwa, ganin haka yasa Abba saurin karasowa kusa dasu yace "sannu mamana, ya jikin naki?" "Uhm uhm dasauki Abba, Abba ina yayana yake  nasan Yana tausayina bazai rabu Dani ba ko?" Gaba kidaya mutanen dake gurin ta basu tausayi ,wani murmushi Abba yayi mai cin Rai ,zuciyarsa na suya kamar zata fashe sabida bakincikin abin da suhail yayi, can Kuma ya tattaro gabaki Daya karfin halinsa ya dafa goshinta hadi da shafo kanta zuwa bayan gashinta Inda ya kwanta a gadon bayanta, Sannan ya tausasa murya yace "mamana !! "

"Naam Abba"

"Kiyi hakuri kinji ,kimaida komai ba komai ba Indai maganar yayankine karki damu Zamu sake zama Dani da sauran 'iyayenki akan maganarku ,yanzu baki da lafiya abu Daya nakeso shine ki kwantar da hankalinki kinji, banason Naga kina sakawa kanki damuwa yanzu Zamu huce gida,

daga yanzu  banason na sake ganinki ko a part din Ihsan ko gurin goggo bana son ki je, iya kacinki dakin Amma, kafin musan matakin da muka dauka akai, yanzu Maza ki tashi mutafi"

Salwa kam tsuruu ytayi Tana kallon Abba domin dukkan abin da yake fada kallon sa kawai take gabaki Daya hankalinta yatafi can duniyar tunanin suhail,komai ya daina mata dadi batasan lokacin da tunanin zuci yafito filiba tace "yanzu yaya wani ka saka?" Bakinciki ne ya tokare zuciyar Abba wato bamashi take sauraraba , tunanin ta kawai tatafiyi akan Big bro,magana ya soma mata yace "mamana Anya kuwa kinason farincikina?"

"Uhm uhm ab Abba inaso mana" ta bashi amsa a takaice .

"To Indai kina son farincikin na daga yau Babu ke Babu Suhail ko tunaninsa ban amince  kiyi ba ,umarnine ba shawara ba, haba so kike ki kashe kanki, ko sokike ubangiji ya kamamu akan haka, mun kasa ruke amanar da d'an uwanmu ya bar mana, in to ba haka nake ba, banabin San raina, muddum mutum yayi ba daidai ba yazama dole na nuna masa kuskurensa , suhail danane Kuma kema 'yatace ,Dan haka bazan bi San Rai na maida ke dakin suhail ba, yaci gaba da wahalar dake ba Dani za a Yi wannan aikin ba, Amma temaka mata ki kamota mutafi gida" yayi maganar Yana nufar kofar fita ,suma sauran su uncle faruq binsa sukayi abbaya har zuwa parking space.

∘∘ı∘∘∘∘∘∘∘∘∘∘∘∘∘∘∘∘∘∘∘

Tom acan bangaren suhail Kuwa part dinsa ya koma ,abin danuya ya ishesa ya masa zabi, gaba daya duniyar sai yaji kamar garwashi Dan zafi, zagaye dakinsa ya shiga Yi ,Yana tunani kwalla fall ta cika idonsa, gajiya yayi da zagaye dakin, Dan haka ya samu kujera ya zauna, dai dai gurin da salwa ta takure ya kurawa ido Yana kallo, sosai ya shiga tunano abin da ya faru, musamman lokacin data furgita gumi nazuba daga fuskarta, tsaki yayi ya buga hannunsa a kujerar har sai da yayi kara, mikewa ya sakeyin yayi, ya cire kayansa hadi da daura tawul ya nufi bathroom Dan yayi wanka, Yana bude kofar bathroom din abin da ya faru tsakaninsa da salwa shiga dawo masa, lokacin da take cewa, "yanzu yaya da nacire kayafa kawai ka tashi ka turo kofar" dakuma lokacin da ta kwanta a kasan gurin tana ta burgima ,tsaki yaja kawai ya fice daga bathroom din ya fasa wankan, Kai tsaye dakin sa ya shiga ya kwanta, borgo ya janyo ya lulluba, Dan sanyi sanyi yakeji, Dan haka ya rufe' idonsa ya soma bacci, sai dai kash baccin ma ya gagaresa ,juyi yashiga Yi a kan gadon ko zai  samu bacci ya daukesa Amma ina Abubuwan sai karuwa suke damuwa ta masa yawa, tashi yayi zaune ya kurawa hannunsa ido hadi da botsa dan karamin bakin sa yace "oh my God,meyasa na haikata haka, yanzu kenan awane hali kanwata take ciki?" Yayi tambayar wa Kansa daidai lokacin da yake tuno salwa tana kuka Tana cewa "yaya mai yasa zaka rabu Dani mai nayi maka, wallahi ina sonka Dan Allah Yaya kada Kai

haka" runtse ido yasakeyi ya furzar da iska daga bakinsa yace "to ni wai mai yasa nake haka, kai karya ne taya zance natsani salwa Bayan ita rayuwa tace, kash bazan iya bacci ba, dolene sai na ganta tukunna , to ai basu dawo ba ,Amma dai bari naje .

Mikewa big bro yayi ya nufi part din su Amma, motar da yaga sun shigane yaganta a parking space,shai dar sun dawo kenan, fuskarsa dauke da murmushi ya karasa dakin Ihsan hadi da tura kofa, bakinsa dauke da sallama ya shiga, amsawa Ihsan tayi mamaki cike fall a fuskarta ,tadaya bangaren Kuma Tana fishi dashi akan sakin salwa dayayi.

Karasawa yayi gefan kujerar dakin ya zauna, kallonsa Ihsan tayi tace "yaya barka da dare ,lafiya na ganka a wannan Daren" "uhm uhm Ihsan su Amma sun dawo?" "Eh sun dawo yaya tun dazu ma" "okay, shiru yayi Yana tunanin abin da zai fada mata domin ya San halin da salwa take ciki batare da ta Gane so yake yaji halin da take cikiba, can Kuma sai yace " Amma dai lafiya ko ya naganki ke kadai ba Kyjin tsorone?"

"Ehy yaya tun dazu sun dawo Kuma lafiya kalau, sai dai Amma tace ummiterh bazata dawo dakinnan da zama ba, mebima barin gidannan za ayi da ita"

"Wa.. wh.. what mai to akai ta ina kenan, ban fahimta ba?"

Suhail ya fada a gigice har Saida Ihsan ta tsorata da lamarin sa, ido ta zaro tace

💋 *SALWA* 💋

*©HAFSAT UMAR DANGORO*

Chapter 10

"Yaya lafiya Naga ka gigice to Kai Maine ruwanka Dan an dauke salwa daga gidannan, ai Kai Daman haka kakeso tun da Daman ka tsaneta"

Jikin suhail ne yayi sanyi Yana rasa abin da zaice ,kawai ya mike ya fita ko sallama bai mata

ba, ita Kuwa tabi bayansa da kallo, Tana son karantar abin da ke damunsa, har ya bar dakin.

Yana fita jikin bangon dakin su Ihsan ya tsaya hadi da dafe Kansa, gaba kidaya yarasa mai zaiyi so yake yaga salwa Amma Babu hali, gashi dare yayi, wata dabara ya tuna ,can Kuma sai yayi Dan murmushi,ya huce bangaren su Amma, sai da yaje daidai bakin kofar ya tsaya, yayi shiru Yana babbuga kofar a hankula Dan sun ruga da sun rufe',cikin bacci Amma taji ana bugun Kofa, mikewa tayi zaune Tana goge idanunta alamar mai Jin bacci, karf ta hada ido da. Salwa ,wadda ta zabga tagumi Tana tunani ,ta kurawa gurin Daya ido, cike da mamaki Amma ta sa hannu ta taba salwa hadi dacewa "lafiya ?' a furgice salwa TA dago fuskarnan tata dauke da damuwa, can Kuma sai ta kakaro murmushi tace "uhm uhm Amma baki bacci ba?" "Ai ke zan tambaya tunanin me kikeyi har yanzu bakiyi bacci ba ,banace ki rage damuwa ba bakyajin magana wallahi" salwa ce ta jiyo bugun kofar da sauri takatse Amma dacewa "Amma kinga ana buga kofa bari naje na bude " tamike zumbur sabi da Kar Amma tacigaba da yimata fada, karasawa tayi bakin kofar ta bude, Nan take idanuwanta sukayi arba da abin kaunar tata Wanda tafi kowa so a rayuwarta, zuciyarta ta dafe sakamakon bugawa da taji tanayi da sauri da sauri, idanuwanta suka kara kanka cewa bakinta yashiga rawa, jitake kamar ta rusa kuka tafada jikinsa sabida farincikin ganinsa ,Amma Kuma da ta tuno da irin wulakancin da yayi mata sai taji kamar ta shararamasa mari ,batare da tace masa komai ba ta juya hadi da mai da kofar ta rufe ta dawo, kan bed din ta koma ta kwanta ,tanajin Amma nace mata "waye?" Batai magana ba sai da ta tabbatar kukan da take ya ragu muryarta ta Dan saitu tukunna tace "Amma Babu kowa kawai nice naji kamar buga kofar ake " "murmushi kawai Amma tayi ta kwanta hadi da girgiza Kai alamar bata yadda da abin da salwa tace ba ,kawai dai ta jine Dan karta kara mata wani damuwar, salwa kam kara kudundunewa tayi har fuskarta ta nannade bargon ta zura a cikin bakinta Dan Kar Amma tajiyo sautin kukanta, sanan ta cigaba da kukanta iya karfinta ,tanayi Tana tunanin wai suhail ita zaice ya tsana.

Shikuwa suhail kasa matsawa yayi daga jikin kofar sakamakon tozali dayayi da abincin da yazo nema, a hankula ya sulale a bakin kofar gurin yayi zaman dirshen Yana tunani, jikinsa duk ya mutu yarasa abin da zaiyi zuciyarsa ta daina masa zafi da radadi, tabbas sai yaji inama ace ya karbi shawarar uncle faruq dayace yaje yayi tunani ko na kwana dayane, ya zu gashinan iya kacin kwana Daya yayi da salwa a rayuwarsa ,Yakasa sukuni balle Kuma ace tsawan rayuwarsa tabarsa tabbas akwai sake, rarrafawa yayi ya sakko daga mattakalar benan ya fice gaba daya daga part din , part dinsa ya nufa ya zauna a falonsa ,tagumi ya zabga yayi shiru Yana tunanin mai zaiyi yaji dadi, can Kuma sai ya tuna da abokinsa samir, wayarsa ya janyo hadi da nemo number samir, domin ita kanta Number sai annemota Dan rabonsa da yayi waya da samir tun ranar da aka daura masa aure da salwa, ya kirashi yake sanar masa ya dawo gida gaba kidaya bazai koma ba sabi da Abba yace idan zai koma dolene yatafi da salwa, shikuma Yana tunanin idan ya tafi da ita ajinsa zai zube, shiyasa ya cewa samir bazai dawo a wanan

lokacin ba, yanzu GA shi ta kwabe masa dolene ya nemi samir.

Bugu biyu samir ya daga hadi da karawa a kunnen sa yace "hi ango ango ango ,ango kasha kamshi wallahi abokina Babu ruwanka ,wato soyayya ta boyeka kamanta damu yayi" sai da suhail ya bari samir ya gama surutansa sanan yayi tsaki yace "kaga da Allah malan ya isheni haka, ka shirya jibi zan dawo U.S akwai magana mai mahimmanci danake so muyi" "to abokina Amma dai da amarya zaka taho ko, ina aunty tamu bata mugaisa mana " bakin cikine ya tokare zuciyar suhail baisan San da yayi tsaki ya katse wayar hadi da hulli da ita yace "shashasha kawai" daga haka Kuma ya sakko kasa daga kan kujerar domin shi zaman kujerar ma yanzu ya addabesa ,in takaice muku karshe dai big bro anan bacci mai nauyi yayi awan gaba dashi.

In the morning 🌅

12:45

Tun da gari ya waye Amma take TA faman rashin salwa akan ta tashi taci abinci Amma kamar Yana magana da gawa ,salwa baccinta kawai takeyi sakamakon jiya da daddare bata samu bacciba ,kara dukan bayanta tayi tace "ummiterh, ummiterh tashi mana" motsi salwa ta danyi,hakanne yasa hankalin Amma ya Dan kwanta Dan farko tayi tunanin Babu Rai ajiiinta, Mika salwa tayi Sannan tadan bude ido suka hada ido da Amma kana tace "Amma ina kwana?" Harara Amma ta wata mata tace "kinsan karfe' nawa yanzu Kuwa, tun dazu nake faman tashinki kinki ki farka yau ko sallar asba baki tashiba ,Anya ummiterh,keda sallah bata huceki kecema mai tashin wasu, gaba daya sabi da namiji kintada hankalinki kallifa duk yadda kika zama daga jiya zuwa yau haba salwa, dan Allah ki kwantar da hankalinki akwai lokaci in sha Allah Nan gaba sai kince dama baki tada hankalinki ba, dasannu Zaki rama Indai namijine, suhail danane Kuma nasan halinsa nasan abin da zai iya da abin da bazai iyaba, Nan gaba dole zaiyi danasa akan abin da yayi miki kitashi kiyi sallah sai kici abinci ,abbanku Yana son ganinki" shiru Amma Tayi tan akallon salwa ,ita Kuwa salwa cewa tayi "Amma lokaci yariga da ya kuremin narasa Yaya har abda ,komai zanyi bazan dawo da yaya cikin rayuwata ba, su Abba sunruga da sun yanke hukunci Kuma kinsan Abba kaifi dayane ,Kuma Nima Koda ace ayanzu za a mai da aurena da yaya suhail bazan yarda ba komai son da nake masa yazama dole na hakura tun da mutumin da ya furta ya tsaneka yafi a irga Babu amfanin sake zama dashi domin nasan bazai taba sonaba har abada', zanyi hakuri na karbi zabin da Allah yasake bani akaro nabiyu ,Indai Abdul alkairine agareni ni na amince da zabin abbanmu " salwa ta karasa maganar hawaye na kokarin fitowa daga idonta , shiru Amma tayi tana nazarin maganar salwa, can kuma sai ta janyota jikinta ta rungumeta tana rarrashin ta,har Saida tayi shiru, sanan ta mike tashiga bathroom.

💋 *SALWA* 💋

*©HAFSAT UMAR DANGORO*

Chapter 11

Mikewa Amma tayi tsam tashiga kitchen domin ta hadawa salwa abin da zataci, kawai kawai ta soya mata da kunun gyda , bayan ta Kammala ne tafito, a zaune tasamu salwa kan dadduma ta idar da salla, karasowa tayi kusa da ita ta zauna sannan ta ajiye mata abincin, murmushi salwa TA sakar mata tace "sannu da kokari Amma nasaki aiki, aini yakamata na girkamiki" "uhm salwa kenan to idan ni ban kula dake na ciyar dake abin da zaici ba wazai kula dake, kenan ma baki daukeni kamar ummanki ba " "uhm uhm Allah Amma ba haka bane kawai dai ... "Kawai dai me? Yanzu dai kici abincin sai ki tashi kisamemu a babban falo.....

Tom bayan salwa tagama cin duk abin da Amma takawo mata, mikewa tayi hadi da bude loka ,doguwar riga ta dakko baka tasaka, sanan ta yafa mayafinta, Allah sarki kallo Daya zakayi wa salwa kasan ta fada, sabi da damuwa fuskar Nan tasake zama 'yar kuyat , tafiya ta somayi a hankula tabar part din Amma,babban falon ta nufa, bakin ta dauke da sallama tashiga anan tasamu ,Amma Abba uncle faruq uncle Kabir duk a zaune ita kadai suke jira, amsa sallamar sukayi fuskarsu dauke da murmushi, itama karasawa tayi TA zauna sannan ta dubesu ta gyshesu amsa sukayi Sannan Abba ya kamo hannunta yace "mamana dawo Nan " komawa kusa da Abba tayi ta zauna zuciyarta nayimata buga alamar fargaba, uncle faruq ne ya shafa kanta yace "ummiterh Allah ya yimiki albarka" "Ameen kawai tace tasake maida kanta kasa, abbane ya sake cewa "mamana kin Yi shiru kin sun kuyar dakai kasa alamun har yanzu akwai damuwa atattare dake ?" Murmushin karfin hali salwa TA kakaro ta kalli Abba tace "ah am uhm Abba Babu komai kawai ina tuna abbanane" "murmushi uncle Kabir yayi yace "to ummiterh mai akayi miki har kike tuno abbanki bayan mu muna raye Kuma kinsan Zamu iya yimiki duk abin da zaiyi miki,karkiji tsoron komai ki fadi duk abin da kikeso zamuyi mikishi Indai bai saba daga addinin muba" "hakane uncle ,kawai ina kewar abbanane, sabi da alokacin da yake raye yayana Yana Sona sai da ya bar duniya Kuma yaya ya tsaneni bayan Babu shi aduniyar, mai yasa Dan Adam yake a hakane, maiyasa zai karyamin zuciya ? Kwallar dake makale a idonta tasamu damar sulalowa zuwa kuncinta ,jikinta narawa ta kankame Abba, Shima Abba rungumeta yayi Yana bubbuga bayanta Yana cewa "kiyi hakuri mamana meyasa har yanzu kika kasa mantawa da suhail bayan shi ya manta dake, look mamana bai kamata ace muna yawan tuna mutanen

da mukasan zamansu acikin zukatanmu ba alkairi bane, ki kalli Abdul Maine laifinsa tabbas nasan shi bazai watsa min kasa a ido ba ,Dan Allah mamana ki hakura da suhail ki karbi zabin da nayi miki" "uhm uhm Abban bawai zabin ne bai min ba wallahi Abba yaya suhail Yana Sona har yanzu ina ganin soyayata acikin idanunsa ,Dan Allah Abba idan har zancire Rai da soyayyar yaya suhail to ku daukeni daga gidannan, nafison natafi can wata kasar nayi rayuwa ni Daya, ina son na manta da yaya abba Dan Allah kuyi min wanan alfarmar in yaso idan nadawo nasamu nutsuwa sai ayi auren da yaya Abdul"

Shiru Abba yayi ya dan nisa kadan sannan ya kalli salwa yace "shikkenan mama na zaki iya tashi ki tafi inshallah zamu zauna da sauran iyayen ki muga me zamu yanke akai, kallon Abba salwa ta danyi kamar tana nazirin wani abu daga bisani Kuma tace"shikkenan Abba"jiki a sanyaye ta mike taso ma tafiya har ta fita gada fallon.

Bayan fitar salwa su abbane suka bi Bayan ta da kallo cike da tsananin  tausayin ta Amma ce tace"u uhm gaskiya ya kama ta a duba lamarin yarinyar Nan me ze hana a bata Wanda take so tun da na fahinci cewar suhail mafa yana sonta ,kawai yarintace ke damunsa , idan akayi haka sainake ganin kamar ba a masu ADALCI ba" "shiiiii ya Isa haka banason maganar banza Indai MAGANACE Akan suhail banason ta yanzu abu guda nake bukata shine ki kawo shawara akan yadda zamuyi yamanta da babun suhail acikin rayuwarta" "haba Abba maiyasa zakace haka wanna hukuncin da aka yiwa suhail yayi tsauri kobabu soyayya inaganin AI akwai zumunci " "ya ci uwarsa zumuncin,shi ba zumuncin ya take ba" zaro ido uncle faruq yayi cike da mamaki Wai yau abbane da zagi gaskiya ransa ya baci,  zancen uncle faruq ya  katse da cewa "ni ina tunanin kawai akai yarinyar Nan makarantar kwana in yaso sai a hadata da soja yana gadinta daga cikin sojojin suhail " jijjiga Kai Abba yayi alamar gamsuwa da maganar  uncle faruq ,sanan yace " yanzu kuna ganin wace makaranta yaka mata mukaita ?" " No ai Bamu yakamata mu yanke wacce za a kaita ba Yakamata muji ra,ayita tazabi Inda takeso mukaita sai tafi samun kwanciyar hankali "cewar uncle Kabir.

Kallon Amma Abba yayi yace " Tom ina gajin ke yakamata ki tambayeta mebi tafi fada miki tun da ke macace batajin kunyarki kamar mu Maza" "toh Amma tace Sannan ta mike ta bar wajan.

Abangaren big bro kuwa akwati Daya ya dauka yazuba iya kayan dayasa  zaiyi amfani dasu idan yaje u,s , mikewa yayi cikin riga dawando farar riga wando Blue mai kyau da sheki, sosai ya masa kyau ya amshi jikinsa, akwatin sa yaja yafita, Kai tsaye part din Amma ya nufa ,dakinta ya nufa domin yasan Babu kowa sai ita, da sallama abakin sa ya karasa sanan ya nemi izinin shiga" salwa Kuwa na zaune a gaban Amma jitake kamar ta tashi tabar gurin da bantason sukara hada ido, wata zuciyar Kuma tace " a,ah ummiterh ki zauna kada kitashi amma tayi tunanin wani abu, daukar shawarar zuciyar tata tayi TA zauna hadi da sun kuyar da kanta kasa.

💋 *SALWA* 💋

*©HAFSAT UMAR DANGORO*

Chapter 12

Shigowa suhail yayi tare da durkusawa a gaban Amma ya gaisheta sanan yace "to Amma ni zan koma" cike darashin fahimta Amma tace "ka koma ina ?" "U.s zan tafi yau dinnan " "u.s Kuma suhail maiyasa ai lokacin da ka dauka bai Kare ba" "eh Amma sonake na tafi akwai wasu Abubuwan dana keson karasawa acan " "okay Babu damuwa Allah ya kiyaye hanya ya tsare ka daga sharrin makiya mahassada kakula kaji" "ameen thumma ameen Amma zamurinka waya idan nakoma " har da zai tashi ya fita Kuma sai yaga salwa tayi shiru ko gaysuwa Babu , sai da ya tattaro duk wani kuzarinsa sanan yace "uhm ummiterh kintashi lafiya ?" Shiru salwa tayi kwallar da take makalewa tashiga gangarowa daga idonta , daker ta iya tattaro kuzarin Daya rage mata tace "in ina... Ina wuni yaya" "lafiya kalau kawai yace ya mike yace "to Amma ni zan huce" daga haka ya juya baya ya soma tafiya, da sauri salwa TA dago jajayen idanuwan ta tace " Amma ki tsayar dashi Dan Allah kada ya tafi ya barni ,uhm uhm yayana Amma kice ya tsaya Dan Allah, salwa TA mike tare da fadawa kan gado ta fashe da kuka, shikuwa suhail tuni ya sauka daga mattakalar dakin ,sai da yayi nisa Sannan ya juyo idonsa ya kada yayi jajur kamar garwashi.

Yana fita daga part a hanya ya hadu da ihsan ta dawo daga school, cike da mamaki ta karaso kusa dashi ganin yadda ya dakko jaka Yana tafiya, da sauri tace "yaya lafiya ina Kuma zakaje naganka da akwati" uhm yayi kwafa tare da sakin murmushin karfin hali sabi da karta Gane yanayin da yake ciki yace "lafiya kalau Ihsan kawai dai zan koma u.s ne " "mai yaya u s Kuma to mazaka komayi acan ?" "Mai zankoma Yi acan Kuma bayan acan nake aiki ,kinsan aurena da ummiterh ne ya dawo Dani TARABA ,to Kuma Daman hutun da na dauka yakusa karewa shiyasa zan koma can kawai " "to ..... Th.. to kenan yaya idan katafi yaushe zaka dawo ?" Tayi tambayar kamar zatayi kuka, "uhm Babu rana Ihsan" daga haka bai sake cemata uffan ba ya shige part din goggo, ita Kuwa Ihsan bin bayansa tayi da kallo fuskarnan tata dauke da mamaki .

Yana shiga falon ya tarar da su Abba zaune suna tattaunawa , karasawa yayi ya gaishesu

suka amsa, Sannan yace "Abba ni zan koma" "okay tom Allah ya tsare " abin da Abba yace masa kenan saka makon haushin sa da yakeji akan sakin salwa da yayi, Shikuwa suhail baiyi mamaki ba Dan Abba bai tambayesa dalilin komawar sa ba,ya mike tsaye zai shiga dakin goggo, uncle faruq yace "lafiya son zaka koma ?" "Uhm Babu komai uncle Kiran ujilane ya sameni shiyasa " "oh Tom shikkenan Allah ya tsare ya kaika lafiya son" ameen kawai big bro yace ya huce dakin goggo, a zaune ya sameta tana cin abinci Abdul nayi mata barkwanci domin shi Abdul ya warke tun da yasamu abar kaunarsa salwa, shiga yayi ya gaisheta Sannan ta amsa, Abdul ne ya kallesa yace "yaya ina wuni?' " lafiya klau Abdul ya jikin naka?" Yayi maganar Yana tsaresa da manyan idanunsa masu kama Dana mage, "da sauki yaya Al nasamu lafiya Amma yaya yanaganka kamar tafiya zakayi?" "Eh zan huce u s ne shine nazo nayi muku sallama" saurin zaro ido Abdul yayi yace "u.. u.s fa yaya" eh u s zan tafi ai Daman acan nake dazama bai kamata kayi mamaki Dan zan koma ba" "toh ... Shikkenan yaya Allah ya dawo dakai lafiya Amma dai zakazo bikina ko?" "Bikinka Kuma, dakai dawa yaushe?" "A,ah yaya bikina da my salwa mana Nan da shekara uku" tsaki suhail yaja kawai ya mike yace "goggo ni na huce " bai jira abin da zatace ba kawai ya fita, zuciyarsa nayi masa wani irin tukuki da zafi.

Azafafe ya fice kamar wani zaki' sukuwa su Abba bin bayansa sukayi da kallo har ya fice, uncle Kabir Kuwa cike da tausayinsa yake kallon bayansa, hakama uncle faruq don su sunsan mai suka hango masa Nan gaba.

Yana fita yasaka akwatin a mota, Sannan ya shiga gidan baya aka jashi zuwa airport, sai da sukayi tafiya mai nisa Sannan suka Isa, airport din ,,tun daga bakin gate sojoji ne burjik suncika airport din sunyiwa wajen da,ira ,a yadda na kalli yawan su Kai kayi tunanin wani mai fada aji ko wani babban mutumin suke jira, sai kawai naga sunzo sun lullube motar da suhail yake ciki, tun kafin ya fito dukkan su kayi layi hadi da kamewa guri guda, Yana sako kafarsa waje dukkansu suka Sara masa , batare da big bro yace komai ba ya huce gaba, shika bishi a baya, jirgin ya shiga ya zauna sa,annan suma suka shiga wani jirgin bawan da suhail yake ciki ba, wan da yake ciki shi kadaine a zaune yayi shiru yarasa abin da yake masa dadi, komai yanzu ya sauya masa kamar ba shine suhail ba, haka dai Tana ta tunani har jirgin su yadaga zuwa u,s.

A can bangaren salwa Kuwa kuka takeyi akan gadon kamar zata shide ,hankalin Amma duk ya tashi , tayi rarrashin Tayi rarrashin Amma ina duk abanza kamar kara kunno salwa take, kuka take Tana cewa "yanzu shikkenan yaya yatashi ,kwarin gywar danake dashi akansa duk ta kau,yanzu kenan ta tabbata yaya baya Sona mai nayi masa Ashe Daman zai iya tafi ya bar marainiyar kanwarsa, Amma ki fadamin meyasa yaya ya nunamin soyayyar karya lokacin ina karama ayanzu Kuma Babu wadda ya tsana sama Dani, laifinanne Dan na sonshi, ko laifinanne Dan kaddara tasa na aureshi ,Amma narasa yadda zanyi da zuciyata wallahi da ace ina da damar sarrafa zuciyata akan son da nake yiwa yaya suhail da tuni na cire domin na fahimci

bana da gurbi acikin rayuwarsa, Abdul ke Sona Abdul masoyina nagaskiya , Dan haka dagayau zan bi umarnin abba na dau damarar yin karatu kodan yadda yaya suhail yake guduna kawai sabi da a kauye aka haifeni ni ba Wayayyiya bace, Indai wayewa ce kada su damu hatta matan gidanan sai na basu mamaki sai na nuna musu ni ba sa,ar su bace,

Abdul ne kadai ke Sona agidannan ,Kuma shi yake mini soyayyar gaskiya ,yasoni tun ina 'yar kauyeta sanan yasoni a yanzu Dana soma sanin waceceni ,zanje karatun na dawo Kuma na auri Abdul bazanyi butulci akan hakaba Amma "

Shiru Amma tayi tana sauraronta can Kuma ya dago tace "tabbas gaskiyar salwa ya kamata ace kicire soyayyar wani da namiji a zuciyarka, ki fuskanci alkibula ki gyra komai na rayuwarki ,ina son kibawa kowa mamaki a cikin gidanan ,ki daure ki koma karatu kinji" "in sha allah Amma zanyi karatu wacce makarantar kuka zubarmin?"  "A,ah zabinki akeso a wace kasa kikeson kiyi karatu ?" Shiru salwa tayi can Kuma sai ta ce " Amma ina son a kaini Dubai " okay shikkenan ai ta kwana gidan sauki ma tun da can kika zaba, akwai wani abokin abban ku acan ,zamuyi magana dashi idan Babu damuwa sai ki zauna a gidansa in yaso sai a hadaki da soja ko biyune suna kula dake ko" murmushi salwa tayi tace "nagode sosai Amma Allah ya kara miki lafiya da nisan kwana, bantaba ganin wadda take fifita soyayyar 'yar Dan uwan mijinta ba akan soyayyar 'yayanta ,Amma ke din ta musammance a gareni " "tooo yaukuma tanan kika bullo ,bana son irin wannan kema 'yatace kamar yadda su Ihsan suke a matsayin 'yayana ,yanzu ki share hawayenki tun da dai Naga kinzama jaruma ,sai kije kiyi wanka ko Kyji dadin jikinki ,ni Kuma bari naje gurin abbanku na sanar masa ga Inda kikeso a kaiki" daga haka Amma ta mike ta fita.

Tana fita dakin Abba ta huce ,kwance ta sameshi ya lumshe ido Yana tunani ,sallah matayi sanan ta karasa gefan gadon ta zauna, a hankula ya bude idonsa yace "hajjau" "Naam ranka ya dade suhail yazo yimuku sallama?" Kai kawai ya daga baice komai ba, Amma ce tasake cewa "yanzu Abba kana ganin wanna tafiyar dayayi asan ransa yayi ta?" "Koh ! Tun da kikaga yatafi Al asan ransa ya koma" "a,ah fa Kai baka fuskanci wani abu daga gareshi ba?" "Mena fuskanta kawai dai na fahimci yazabi komawa ne akan mun takura saiya zauna da mamana" "a,ah Abba ba haka bane kayi wa abin mummunan kallo, ni ayadda na fahimta son da yakewa ummiterh ne yasa ya bar gidannan sabi da idan yaganta Yana tunawa dacewa ka mallakawa Abdul abin da yafi so a rayuwarsa" hannu Abba ya daga mata Sannan yace" ya Isa haka ,idan har akan wanna maganar ne ya kawoni Zaki iya tafiya" Abba ya hade rai yayi kicin_kicin, " uhm Al abin bai Kai hakaba daman maganace akan ummiterh  game da makarantar da kace tazaba wane gari yakeso" "okay ina jinki tazabi makarantar ne?" "Eh tace tanason a kaita Dubai idan da dama, sai a nema mata wajan kwana, ni Kuma sai Naga Al kana da aboki acan shine nace mai zai hana ta zauna a gidansa har Allah yasa ta Kammala karatun ta" Kai kawai Abba yadaga alamun gamsuwa da maganar Amma sai da yayi shiru na dan wasu lokuta Sannan yace "okay babu damuwa insha Allah zuwa gobe zan kirashi namasa magana ,kice mata ta shirya Nan da sati daya Zamu tafi" amsawa tayi da to sanan ta mike tayi masa sallama ta fita.

💋 *SALWA* 💋

*©HAFSAT UMAR DANGORO*

Chapter 13

Zarace tashigo dakin da gudu har tuntube take gurin bude kofar , a razane zubaida ta mike hadi da cewa "ke lafiya?" Duk gaba dayansu suka bi Zara da ido, "lafiya ba lafiya ba, yaufa big bro ya koma u.s " "what? Zubaida da mufida suka mike zumbur, ban fahimta ba wai kina nufin yanzu yaya baya gidan Nan ,to mai yasa zai tafi Al naga hutun da ya dauka bai Kare ba?" Dariya zarah ta kwashe Dashi tace "mai zai sa yatafi Kuwa ban da wanan abin da ya faru, ai nafada muku wallahi Yaya Yana son salwa kawai dai Yana nuna bayayi ne Dan Kar ta raina shi, zai zaunane bakinciki ya kasheshi Yana gani ya Abdul ya aureta " wani wawan Mari zubaida ta tsinka mata hadi da cewa "to uban waya saki ,har da zakizo kina fadamin wai sabi da Yana sonta ya tafi ,aini gwara da yatafi din yadda zan Fi lakadawa shegiya duka, ko ya kikace Ameera?" Dariya Ameera tayi tace ,wallahi Nima nasamu dama ,tun da ya Abdul bashi da lafiya kullum Yana daki a kwance Nima nasamu da mar da zan nakasa shegiya kowa ya huta......

"Uhm a banza tun da haryanzu ihu ake abayan hari,inga aiki da cikawa kawai shine zan tabbatar da son da kikewa ya Abdul"Zarah ta fada hadi da hurgawa Ameera harara, ",kan uba ni kike fadawa haka wato har raini ya soma shiga tsakanina dake, Ameera ta Kai mata duka Afusace, fuzge hannunta tayi daga rukon da Ameera tayi mata tace "karki kara dukana na fada miki ,karkiga ni kanwarkice kice Zaki dakeni na kyleki wallahi ramawa zanyi" "au yanzu zarah ni kike cewa idan na dakeki Zaki rama, wato raini har yakai haka, dafarko nace inason ya Abdul kema kince kina sonsa na hakura na zuba miki ido Naga iya gudun ruwanki, shine yanzu har dakin rashin kunya to bari ya huzaifa ya dawo wallahi sai kin raina kanki" daga haka Ameera ta bangajeta tafice daga dakin zuciyarta nayi mata zafi.

Tom bayan fitar Amma daga dakin, abbane ya dauki wayarsa ya Danna wata number bugu Daya zuwa biyu aka daga hadi da yin sallama "assalamualaikum" "wa alaikumussalam Alhaji YUNUS kana lafiya?" "A,ah lafiya klau alhamdulillah Alhaji LAMIN Daman ana jinka kanan, Kai ka manta da mutane haba ,rabona da na ganka tun rasuwar d'an uwanka ABDULHAMEED, gaskiya baka da kirki wallahi" dariya Abba yayi yace "wallahi inan abubuwane sun mun yawa Kuma ga busy duk na shiga shiyasa Amma dai yanzu kana lafiya?" "Lafiya kalau alhamdulillah

ya yaran ina uban Muskilanci shugaban kywawa" alhaji yunus ya yayi tambayar Yana dariya, murmushi Abba yayi yace "Kai kyleni da Sha,anin yarannan Yan bana bkwai ka haifesu baka haifi halinsu ba, ya yaran gurinka" "sunnan lafiya kwanaki kausar tayi nacin na barta yazo gurin Ihsan tasamu hutu Kuma Allah bai yiba" "bawani nan Kai ka hanata zakace wani hmm" Abba yayi shiru, "uhm ba haka bane wallahi ina Kuwa yarinyar Nan 'yar wajen murugayi kuna Kuwa zuwa dubata?" "Uhm ai nadawo da ita gurina tun ranar da Zamu taho da ita muka taho ,Kai ma kasan ina da yadda zanyi na rike ta bazan barta acan TA wulakanta ba, yanzu ma magabarta ce ta sa na kira ,ina son zata zonan kasar karatu shine nace to Dana kama mata daki a waje ai gwara ta zauna a gidanka sai hankalina yafi kwanciya duk da nasan halin salwa baza ta taba watsa min kasa a ido ba"  washe baki alhaji yunus yayi yace "ah gaskiya kayi dabara mai kyau ,tun da dai  muna kasar kawai ta zauna din Babu matsala yaushene zata soma karatun ?" "Eh dai Nan da sati guda nakeson komai ya kankama insha Allah dakaina zan kawota ,in yaso sai na dawo" Tom godiya Abba yayiwa alhaji yunus sosai sann sukayi sallama Abba ya kashe wayar.

*Dubai*

Kausar da ke kusa da mahaifinta CE ta kalli Abba ta wan da ya gama waya yanzu, Daman tun da taji cewar da abban TARABA yake waya tashiga murna tadawo kusa dashi domin taji mai za ace, Yana katse wayar tace "Abba wai Ihsan ce zata zo karatu Nan?" Tayi maganar taba dariya alamar murna, domin kausar su biyu Allah ya bawa alhaji yunus,daga ita sai yayanta namiji Shima baya kasar shekara 3 da suka huce, shiyasa ta damu taje TARABA kodan ta samu kawar hira, tun da agidan su ba fita take ba, sai dai ta zauna a gida tayi shiru ,ko Kuma ta zauna da Momynta ita kuma batason hira da mahaifiyar ta sabi da ba komai ne zakace zakana hura da mahaifiyar ka akai ba, alhaji yunus ne ya kalli yar tashi yace "Uhm mamana ummiterh ne zata zo 'yar wajen murugayi ba Ihsan ba" baki kausar ta washe hadi da cewa " lahhh Abba wannan yarinyar kekkewa ita?" "Eh eta mana " ya bata amsa a takaice, "WALLAHI Abba inason yarinyar Nan Tana burgeni Abba kaga dai 'yar kauyece Amma kwata kwata batayi kala da kauyawa ba, kamar ba a kauye ta taso ba, wai yanzu Abba ya kake ganin yarinyar Nan idan akace ta dawo burni AI sai tasa Maza suna rigima akanta" dariya alhaji yunus yayi hadi dacewa "kin ganki ko sai wani zuzuta mace 'yar uwarki kike, to shikkenan ki kwantar da hankalinki Indai salwa ce sai kin gaji da ganinta " wani tsalle kausar Tayi ta fada jikin abbanta Tana murna ,"a,ah karfa ki karyani mamana ke bikisan kin girma ba ne to saina kira nace bamanan ta fasa zuwa ma" saurin daga abban nata tayi tace "Dan Allah Abba kayi hakuri kada ta fasa zuwa" tayi maganar kamar zatayi kuka, "a,ah to yaukuma anji kanku keda abban naki kenan " kausar taji maganar ,dasauri ta daga kanta, hango Momynta tayi tana kokarin zama , da gudu ta fada jikinta Tana dariya tace "Momy albishirinki?" "Goro " "fari ko ja?" "Fari fata shalelena" "to Nan da sati daya ummiterh zata zo Nan karatu" "kai Dan Allah dagaske kike ?" "Allah dagaske nake Momy yanzu Abba yagama waya da abban TARABA " dariya Momy tayi hadi da cewa "oh kace su kausar an samu abokiyar zama sai Kuma abin da ya karu ko " Dan tsuke fuska kausar tayi tace "uhm uhm Kai Momy Maine zai faruto?" "A,ah rashin jinki zai karu mana , hakama ya lafiyar kura ballantana Kuma kin samu kawa, Dan ma ita yarinyar Nan akwai nutsuwa duk da

ban zauna da ita ba" "uhuhm uhm Momy mai kike nufi kina nufin dai ni bani da nutsuwa kenan?" Tayi maganar hadi da mikewa zuciyata cike da bacin Rai wai ita a lallai taji haushi ta shige dakin ta .

Bayan shigar ta Momy ce ta kalli alhaji yunus tace "Abban najib wai dagaske ne salwa zata zo Nan karatu ,banaji ance an daura aurenta da suhail ba ko karyane?" "Uhm kinjiki Daman ana wasa da aurene da gaskene anyi auren ummiterh da suhail watanni uku dasu ka huce" "to Amma Kuma zata zo Nan karatu mai zaisa bazata zabi us ba tun da shi big bro acan yake da zama, Anya kuwa auren yanan" "kinga zainab bana son shashan ci ina ruwanki da aurensu ita Nan ta zaba idan Kuma gidan kine bakison TA zauna sai ki fada naji" "a,ah ni fa bance ba ,ni Kuwa nakeson ummiterh ,haka kurum yarinyar take burgeni ,Daman abin da yasa nake tambaya wai da ita auren ne ya mutu sai mu hadata da najib Naga yarinyar akwai nutsuwa" "uhm Abba yayi kwafa yace "to idan auren bai mutu ba saiki kasheshi " yayi tsaki ya mike ya shige daki ya bar Momy a gurin a zaune . "Uhm kwama gama boye boyen ku Indai nice saina gano komai a to " itama daga haka ta mike tashiga nata dakin.

*U.S*

Tun da jirgin su big bro suka tashi basu sauka ba sai misalin karfe' 2:30 na washegari ranar da suka tafi, Kai tsaye babban gurin saukar jirgi na kasar us jirginsu ya sauka, tunkan su isa ilahirin yaran sa dama manyan sojoji masu fada aji suka tsaye domin tarbar sa, sosai filin jirgin ya cika da sojoji in da kasan wani babban Dan soyasane yazo ko shugaban katsa, ni abin har mamaki ya soma bani yadda Naga Dan karamin yaro Yana bawa mutane umarnin da mulkarsu, ban gushe daga tunanin da nake ba, na hango wani kekkewan saurayi sanye da riga da wando wadan da suka karbeshi suka haskashi yayi kyau sosai abin sau wan da yagani , glas din sake idonsa na kalla baki wulik baka iya ganin yanayin idonsa sai dai shi ya ganka, a sannu yake takowa daga cikin jirgin Yana taka mattatakalar cikin nutsuwa da takama, gefe guda Kuma samir ne tsaye Yana sakar masa murmushi, da matarsa da Kuma kannen sa guda biyu mata, Daya daga cikin 'yan matan ne ta kalli dayar tace "ke Salma wai bakiga yadda yaya ya kara kauba wow Amma fa wannan gayen ya hadu" "hade rai wadda aka kira da Salma tayi tace "aikin banza abin da mun rasashi kina dai ji yaya samir tace aure akayi masa, dalilin komawar sa guda kenan, ai wallahi tsofaffin Nan nasa basu kyau ta mana ba, haba Shima kamar wani ba wayeyyeba Yana da class Amma bazai tsaya ta zabi mai aji ba" "uhm ni dai ban hakura ba wallahi idan ma ke kin hakura ato Dan wallahi saina aureshi, cewar halima "to taya kenan" "hmm Salma kenan ai Allah ya halatta nasa ya auri mata Daya Daya Daya Daya har hudu ,Kuma dai kinsan waccan matar cushe ce nikuwa zuciyarsa zan sace, ke baki samu labarin bakwauyiya ya aura ba? "Au wai Dan Allah dagaske 'yar kauye ce"... "Hmm muje gida Kisha labari ai naji lokacin da shi suhail din yake fadawa yaya samir cewar baya sonta mai zaiyi da 'yar kauye

End book 1

09166764540 HAFSAT UMAR DANGORO
Paid book #500 KACAL